# GABATARWA

## Da sunan Allah Mai Rahama Mai Jinƙai

Dukkan yabo da godiya da jinjina da kiraari da kuma neman yarda sun tabbata ga Allah Maɗaukaki. Muna jaddada godiyarmu gareShi a bisa ni'imomin nan naShi marasa ƙididdiguwa. Kuma muna neman taimakonSa ako da yaushe (kuma akan komai). Muna kuma neman GafararSa. Muna kuma neman tsarinSa daga sharrorin kawunanmu da kuma miyagun ayukanmu. Muna roƙon Shi da Ya sanya mu cikin bayinSa waɗanda Ya shiryar, Ya kuma tabbatar da mu akan wannan Tafarki na Shiriya har mutuwa (har abada). Tsira da Amincin Allah su ƙara tabbata ga ManzonSa Muhammadu, shi da iyalansa da Sahabbansa, da sauran duk waɗanda suka biyo bayansu da kyautatawa, har zuwa ranar sakamako. Da fatan Allah Yasa mu ma muna cikinsu.

**Bayan haka**:
Sanannen abu ne dai kowa daga cikinmu yana aikata laifi. Mu duka muna da zunubai, domin kuwa muna saɓa wa Allah ﷻ dare da rana. Saboda haka kowannen mu yana da matuƙar buƙaatar samun Gafarar Allah Mabuwayi Maɗaukaki, don ya samu rabuwa da waɗannan zunubai da yake kannaɗe dasu ko ta ina.

Daga cikin Rahamar Allah ga bayinSa, Ya yawaita musu **Hanyoyin Samun GafararSa**. Kuma babu wanda zai bi su fahce sai Ubangiji Mabuwayi Mai Jinƙai Ya game shi da GafararSa, kuma sai Ya lulluɓe shi da yalwatacciyar RahamarSa wacce ta wadaci komai.

Haƙiƙa mai lafiyayyen hankali daga cikin mutane shi ne wanda yake gaggawar komawa ga Majiɓincin al'amuran kowa da komai, ta hanyar riƙo da hanyoyin samun Gafararsa (waɗanda babu makawa sai an bi su kaafin a samu biyan buƙata).

Ya ɗan-uwa mai girma! Insha'Allahu Waɗannan 'yan shafukan da kake dab da fara karantawa za su ƙunshi bayani akan wasu daga cikin Hanyoyin Samun Gafarar Allah (ga duk wanda yabi su kamar yadda Shari'a tayi bayani). Da faatan Allah ﷻ Yasa mu cikinsu.
Allah Yasa mu dace.

Hanyoyin samun Gafara suna da matuƙar yawa sosai. Amma zan kawo mana guda goma daga cikinsu insha'Allah, daga cikin waɗanda malamai masu yawa sun nuna cewa su ne sukafi muhimmanci.
Su ne kamar haka:

- Tuba;
- Neman gaafara;
- Shiga Musulunci;
- Nagartaccen Imani;
- Biyayya ga Manzon Allah, da nisantar saɓa masa;
- Sauran ayuka nagari (irinsu rukunan Musulunci da sauransu);
- Haƙurin bawa a bisa wata jarrabawar da ta same shi;
- Addu'ar Mumini ga Mumini (musamman roƙa masa gafara);
- Ceton Manzon Allah a gobe Kiyamah;
- Afuwar Allah ga wanda Ya ga dama cikin bayinSa..

Waɗannan dai su ne manyan kashe kashen. A ƙarƙashin wasu daga cikinsu kuma akwai wasu ƙananan kashe-kashe, waɗanda za a ga kowanne a wurinsa Insha'Allahu.
Da farkon fari zan fara da roƙon Ubangiji Maɗaukaki Ya arzukta ni da ikhlasi Ya kuma datar dani wajen gabatar da abinda Zai yarda dashi, Yasa shi a mizanin kyawawan ayuka, kuma Ya Gafarta mana laifukanmu da kurakuranmu (daga mu har iyayenmu da iyalanmu da malamanmu da duk sauran 'yan-uwa mu musulmi baki ɗaya).

Ina roƙon Allah Mai Karimci Ya sanya mu baki ɗayanmu cikin bayinSa masu tsoronSa, masu tsare dokokinSa, masu lafiyayyen hankalin nan waɗanda suke tuban gaske su koma gareShi..

Allah Yasa mu cikin masu kyautata niyyah a yayin aikata duk wani aikin da muka sa a gaba, da kuma baki ɗaya abinda zamu furta.

Allah Yasa mu cikin bayinSa waɗanda Ya tsare su daga sharrin shaiɗan, kuma Ya kuɓutar damu daga aikata duk abinda zai jawo mu afka cikin fushinSa da uƙubarSa a duniya da lahira. Lallai Shi Majiyi ne, kuma Mai amsa roƙon bawa.

Ɗan-uwanku a Musulunci:

**Musa Muhammad Sallau Jada**

(Aboomaryam Aljaadawiy)

## (Hanyoyi Biyu Na Farko)
## Tuba, da kuma Neman Gafara

Kalmar **Tuba** tana nufin: komawa ga Allah ta hanyar nisantar ayukan saɓo, da kuma neman yafiya daga gareShi.
Ita ma kalmar **Istighfari** tana nufin neman gafarar Allah daga zunuban da bawa ya aikata. Allah ﷻ Ya umurce mu da mu gaggauta Tuba zuwa gareShi. Kuma Ya yi alƙawrin Zai Yafe mana zunuban mu matuƙar munyi hakan. A cikin Suratut-Tahrim (ayah ta 8) Allah ﷻ Yana cewa:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ تُوبُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ تَوۡبَةٗ نَّصُوحًا عَسَىٰ رَبُّكُمۡ أَن يُكَفِّرَ عَنكُمۡ سَيِّـَٔاتِكُمۡ وَيُدۡخِلَكُمۡ
جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ يَوۡمَ لَا يُخۡزِي ٱللَّهُ ٱلنَّبِيَّ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَعَهُۥۖ نُورُهُمۡ يَسۡعَىٰ بَيۡنَ أَيۡدِيهِمۡ
وَبِأَيۡمَٰنِهِمۡ يَقُولُونَ رَبَّنَآ أَتۡمِمۡ لَنَا نُورَنَا وَٱغۡفِرۡ لَنَآۖ إِنَّكَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ٨ ﴾

"*Ya ku waɗanda sukayi imani! Ku tuba zuwa ga Ubangijinku tuba irin na gaskiya. Akwai tabbacin cewa Ubangijinku Zai kankare muku munanan ayukan ku, kuma Zai shigar da ku Aljannatai waɗanda koramu ke gudana a ƙarƙashinsu. A wannan rana Allah ba Ya kunyata Annabi da waɗanda sukayi imani dashi. Haskensu yana gudana ta gabansu da kuma bangarorinsu na dama, suna cewa Ya Ubangijinmu Ka cika mana haskenmu, kuma Kayi mana Gafara, domin kuwa lallai Kai ne mai iko akan dukkan komai*".

Mu gaggauta tuba, mu yawaita neman gafara. Domin kuwa **"Duk wani ɗan Adam mai kuskure ne. kuma mafiya alkhairi daga cikin masu kuskuren nan, su ne masu tuba[1]."**

Manzon Allah ﷺ dai shi yafi kowa yawan Istighfari, tareda kuma shi yafi kowa matsayi gun Allah ﷻ, haka kuma shi yafi kowa tsoron Allah ﷻ da kuma tsare dokkinSa.

---

[1] (Ahmad: 13072), (Tirmidhi: 2499), (Ibn majah: 4251) Daga Sahabi Anas ɗan Malik ؓ

Allah ﷻ Ya tabbatar masa cewa Ya riga Ya yafe masa duk wani abinda ya gabata na zunubansa[2] (ballentana da ma bai yi ba), Ya kuma yafe masa abinda zai yi nan gaba ma (tare da kuma ba zai taɓa yin laifi ba har abada) amma duk da haka ya fi kowa neman gafarar Allah ﷻ. Akullum kuma ya kasance yana ƙara zaburar da al'ummarsa wajen dagewa akan haka sosai da sosai. Ingantattun Hadisai masu yawa sun tabbatar da hakan, cikin manyan littafan Hadisi daban daban. Shi da kansa ma yake cewa: "**Wallahi ni (da kaina) ina Neman Gafarar Allah kuma ina Tuba zuwa gareShi sama da sau 70 a yini guda**[3]"

Manzon Allah ﷺ yana ma yin Istighfari sau ɗari a zama guda, banda waɗanda yakeyi a sauran wurare da lokuta daban-daban. Sahabbai suka ce a duk inda ya zauna, yana yawaita faɗin:

رَبِّ اغْفِرْ لِي وَتُبْ عَلَيّ، إِنّكَ أَنتَ التَّوّابُ الرّحِيمُ

**"Ya Ubangiji Kayi min Gafara kuma ka karɓi tuba na, domin kuwa Kai ne Mai Yawan karɓan tuan nan, Kai ne kuma Mai JinKai"**

Sahabi Abdullahi ɗan Umar (Allah ƙara yarda dasu) yace sun kiyaye Manzon Allah ﷺ yana maimaita wannan addu'a har sau ɗari a zama guda[4].

Manzon Allah ﷺ yace "**Ya ku mutane! ku Tuba zuwa ga Allah kuma ku nemi GafararSa. domin ni ma (da kaina) ina Tuba zuwa gareShi har sau ɗari a rana**[5]"

Allah ﷻ Ya yi alƙawarin Gafarta wa duk wanda ya Tuba ya koma gareShi. Kuma Zai sanya shi cikin waɗanda Yakeso, domin kuwa Yana son masu Tuba.

---

[2] Duba: Suratul-fat'hi ayah ta biyu (2)
[3] Bukhari (hadithi na 6307), daga Sahabi Abu-Hurairah ﷺ
[4] Duba: Sunan Abi-Dawud (hadithi na 1516) Hadithi ne ingantacce.
[5] Saheeh Muslim (Hadithi na 2702). Daga Sahabi Al-Agharru ɗan Yasaaru ﷺ

Ya faɗi hakan ne a cikin Suratul-Baƙara (ayah ta 222) inda Yake cewa:

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلتَّوَّٰبِينَ وَيُحِبُّ ٱلْمُتَطَهِّرِينَ ﴿٢٢٢﴾ ﴾ [البقرة: 222]

*"..Lallai allah Yana son masu yawan tuban nan, kuma Yana son masu (kyautata) tsarki."*

Saboda irin tsantsar Son da Allah ﷻ Yake wa masu Tuba zuwa gareShi ma, Yana matuƙar farin-ciki[6] sosai da bawanSa idan har ya tuba ya koma gareShi, fiye da irin farin-cikin da ɗayanmu zai yi idan dabbarsa ta gudu da abincinsa ta bar shi a tsakiyar daji sannan sai ta dawo gareshi a daidai lokacin da ya gama ɗebe tsammanin ci gaba da rayuwa[7].

Saboda haka aka umurcemu idan muka gama alwala mu riƙa cewa:

اللَّهُمَّ اجْعَلْنِي مِنَ التَّوَّابِينَ وَاجْعَلْنِي مِنَ الْمُتَطَهِّرِينَ

"Ya Allah Ka sanya mu cikin (bayin nan naka na gari) masu yawan tuba, Ka kuma sanya mu cikin masu tsarki[8] (waɗanda Kace Kana son su)"

Allah ﷻ Yace Yana son masu tuba su koma gareShi, kuma Yana son masu kyautata tsarki. Wannan kaɗai ma isa ya zama dalilin da zai sa mu gaggauta tuba.
Sanannen abu ne Tsarki mafi girma shi ne tsarkakuwa daga dattin shirka da kafirci da munafunci, da ƙazantar zunubai da dauɗar miyagun ayuka.
Toh tuba zuwa ga Allah ﷻ da kuma neman gafararSa, suna daga cikin manya-manyan hanyoyi na samun irin wannan Tsarki mafi daraja.

---

[6] Farin ciki irin wanda ya dace da Shi Allah ﷻ.
[7] Bukhari (**6309**), Muslim (**2747**). Daga Sahabi Anas ɗan Malik ؓ
[8] Tirmidhi (Hadisi na 55) Daga Sayyidina Umar ؓ

Wannan dai a taƙaice shi ne bayani akan tagwayen hanyoyin nan biyu na farko daga cikin **Hanyoyin Samun Gafarar Allah ﷻ,** wato **Tuba Da Kuma Istigfari.**

Da fatan Allah ﷻ Ya sanya mu cikin bayin nan naShi waɗanda Yakeso, masu kyautata tsarki (na bayyane da na ɓoye) kuma masu Tuba su koma gareShi Tuba na gaskiya.

***

## (Hanya ta uku)

## Shiga Addinin Musulunci, da kuma kyautata shi

Musulunci shi ne mafi girman ni’imar da Allah ﷻ Yayiwa bawanSa. Shi ne kaɗai tafarkin da bawa zai bi don ya samu Alkhairan duniya da lahira. Shi ne kaɗai Tafarkin tsira. Shi ne kaɗai yardajjen Addini a wajen Allah ﷻ. Domin kuwa Shi Ya bada tabbacin hakan acikin LittafinSa Mai Tsarki. Acikin Suratu Ali-‘Imran (ayah ta **19**) Allah ﷻ Yace:

﴿ إِنَّ ٱلدِّينَ عِندَ ٱللَّهِ ٱلۡإِسۡلَٰمُۗ ﴾ [آل عمران: 19]

“*Lallai Musulunci shi ne kaɗai (karɓaɓɓen) Addini a wajen Allah* ﷻ”

Acikin dai Suratu Ali-‘Imran ɗin, Allah ﷻ Yace ba Zai karɓi aikin duk wanda ya bauta maSa da wani addini koma bayan Musulunci ba. Ya faɗi hakan ne a cikin ayah ta **85**, inda Yake cewa:

﴿ وَمَن يَبۡتَغِ غَيۡرَ ٱلۡإِسۡلَٰمِ دِينٗا فَلَن يُقۡبَلَ مِنۡهُ وَهُوَ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ مِنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ ٨٥ ﴾

“*Kuma duk wanda ya riƙi (wani tafarki na daban) koma bayan Addinin Musulunci, toh fa ba za a karɓa daga gareshi ba. Kuma shi ɗin a (ranar) lahira zai kasance cikin hasararru*”

Musulunci sharaɗi ne babba daga cikin manyan sharuɗan karɓan duk wani aikin da bawa zai gabatar a rayuwarsa. Shi ne kuma hanya mafi girma daga cikin hanyoyin samun Gafara. Dole kuma sai bawa ya bi wannan hanya (kuma ya inganta ta) kafin sauran hanyoyin ma su amfane shi.

Daga cikin dalilai mafiya ƙarfi akan hakan, Allah Ya kira musulunci da sunan **tuba** a cikin wasu gwala-gwalan ayoyi na Al-Kur’ani Mai girma. Ga kaɗan daga cikin misalai gameda hakan insha’Allahu.

A cikin Suratut-Taubah (ayah ta **5**) Allah ﷻ Yana cewa:

﴿فَإِن تَابُوا۟ وَأَقَامُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَوُا۟ ٱلزَّكَوٰةَ فَخَلُّوا۟ سَبِيلَهُمْ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ۝٥﴾

"*Idan har (kafiran nan) suka tuba (suka musulunta) kuma suka tsaida sallah sannan suka bada zakkah, toh ku rabu da hanyar su (ku ƙyale su, kar ku yaƙe su). Domin kuwa Allah Mai gafara ne mai jinƙai*"

Allah ﷻ Ya hana mu yaƙarsu, saboda tuban da sukayi daga kafircin nasu. Daga tuban nan da sukayi dai, toh shi kenan sun zama 'yan-uwan mu na addini.

Shi yasa a wata ayah ta daban kuma[9] Yake cewa:

﴿فَإِن تَابُوا۟ وَأَقَامُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَوُا۟ ٱلزَّكَوٰةَ فَإِخْوَٰنُكُمْ فِى ٱلدِّينِ ۗ وَنُفَصِّلُ ٱلْـَٔايَـٰتِ لِقَوْمٍ يَعْلَمُونَ ۝١١﴾

"*Idan har **suka tuba** (suka bar kafircin nasu) kuma suka tsaida Sallah sannan suka bada Zakkah, toh (daga nan) sun zama 'yan-uwanku na addini. Kuma Muna rarrabe ayoyin nan ne (dalla-dalla) ga mutane don su sani*"..

Acikin Suratul-Furƙan ma, Allah ﷻ Ya kira Musulunci da da sunan **Tuba**, a inda Yayi bayanin halayen bayinSa na ƙwarai. Yace su ne waɗanda basu shirka kuma basu kisan kai sannan kuma basu yin zina.
Sai Yayi bayanin munin laifin duk wanda ya aikata waɗannan miyagun ayuka masu halakarwa a duniya da lahira, domin kuwa za a ninka azaba ga duk wanda ya aikata su.
Sannan sai Yace:

---

[9] At-Taubah (aayah ta 11)

﴿ إِلَّا مَن تَابَ وَءَامَنَ وَعَمِلَ عَمَلًا صَٰلِحًا فَأُوْلَٰٓئِكَ يُبَدِّلُ ٱللَّهُ سَيِّـَٔاتِهِمْ حَسَنَٰتٍ ۗ
وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿٧٠﴾ وَمَن تَابَ وَعَمِلَ صَٰلِحًا فَإِنَّهُۥ يَتُوبُ إِلَى ٱللَّهِ مَتَابًا ﴿٧١﴾ ﴾

"*..Sai kaɗai wanda ya tuba (daga cikinsu) kuma yayi imani kuma ya aikata aiki na ƙwarai, toh (irin) waɗannan za a sauya munanan ayukansu zuwa ga kyawawa (za a yafe musu zunubansu, kuma a maye gurbinsu da ladan kyawawan ayuka). Saboda Allah Ya kasance Mai yawan Gafara kuma Mai Jinƙai.. kuma duk wanda ya tuba kuma yayi aiki na ƙwarai, toh lallai (haƙiƙa wannan) ya koma ga Allah matuƙar komawa*".

A Suratul-Anfal (ayah ta 38) Allah ﷻ Yana cewa ManzonSa ﷺ:

﴿ قُل لِّلَّذِينَ كَفَرُوٓا۟ إِن يَنتَهُوا۟ يُغْفَرْ لَهُم مَّا قَدْ سَلَفَ وَإِن يَعُودُوا۟ فَقَدْ مَضَتْ
سُنَّتُ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿٣٨﴾ ﴾

"*Kace wa waɗanda suka kafirta in har sun hanu (sun tuba sun daina wannan kafircin nasu) toh za a gafarta musu (duk) abinda ya gabata (na zunubansu). Idan kuma suka koma (suka cigaba da kafircin nasu bayan sun ce sun tuba), toh haƙiƙa hanyar mutanen farko (kafiran da suka gabata a tarihi) ya riga ya shuɗe (za Mu yi musu irin yadda Mukayiwa magabatan su a kafirci)*"

In har wannan shi ne alƙawarin Allah ga kafirai in har suka tuba daga kafirci, ashe kenan mu Musulmi mu ne muka fi dacewa muyi gaggawar komawa gareShi gaba ɗaya saboda mu rabauta. Babu ko shakka Musulunci yana daga cikin manyan hanyoyin samun Gafara. Domin kuwa yana rusa duk laifin da bawa yayi kafin musuluntarsa (yana shafe duk zunubin da bawa ya aikata acikin kafirci).

Haka Manzon Allah ﷺ Ya faɗa wa Sahabinsa Amru ɗan 'As ﵁, inda yake ce masa:

**"Shin baka san cewa musulunci yana rusa duk wani abinda ya kasance kafin shi (na zunubai) ba?[10]"**

Mun gode wa Allah Ta'ala akan wannan babbar ni'ima ta Addinin musulunci. Muna fata Allah Ya raye mu akan ta, Ya tsare mana imanin mu, Yasa mu cika da imani, yasa mu cikin bayin nan naShi masu rabauta a duniya da lahira.

***

## (Hanya ta Hudu)

[10] Duba Saheeh muslim (hadithi na: 121)

# Nagartaccen Imani

Imanin gaskiya, shi zai sa bawa ya tsaida ingantaccen Tauhidi. Shi zai sa bawa ya tsare dokokin Allah ﷻ. Shi zai sa bawa ya nisanci saɓon Allah (sawa'un a bayyane ne ko a ɓoye). Imani yana kuma daga cikin manyan hanyoyin samun Gafarar Allah ﷻ.
Idan muka duba wasu ayoyin Al-Kur'ani Mai Girma, za mu ga inda Allah ﷻ Yake yabon wasu bayinSa masu gaskiya cikin imaninsu, cewa su kam suna ma yin tawassuli da imanin nasu wajen neman GafararSa (da kuma neman tsarinSa daga azabar wuta a gobe ƙiyamah).
Wannan yake nuna ashe nagartaccen imani ma yana daga cikin hanyoyin samun gafara, tunda har ana tawassuli da shi wajen neman tsira a duniya da lahira.

Za mu ga misalign hakan a cikin Suratu Ali-Imran (ayah ta: **193**), inda Allah ﷻ Yake cewa (a harshen bayinSa masu imani):

﴿ رَّبَّنَآ إِنَّنَا سَمِعۡنَا مُنَادِيٗا يُنَادِي لِلۡإِيمَٰنِ أَنۡ ءَامِنُواْ بِرَبِّكُمۡ فَـَٔامَنَّاۚ رَبَّنَا فَٱغۡفِرۡ لَنَا ذُنُوبَنَا

وَكَفِّرۡ عَنَّا سَيِّـَٔاتِنَا وَتَوَفَّنَا مَعَ ٱلۡأَبۡرَارِ ١٩٣ ﴾

Allah ﷻ Yace (su waɗannan Muminai suna cewa): "*Ya Ubangijinmu! Lallai mu mun ji wani mai kira yana kira zuwa ga imani, yana cewa kuyi imani da Ubangijinku, mu kuma sai mukayi imani (kamar yadda ya umurce mu). Saboda haka (muke roƙonKa) Ya Ubangijinmu Ka Gafarta mana zunubanmu, Ka kankare mana munanan ayukanmu, kuma Ka karɓi rayuka mu tare da mutanen kirki (masu yi maka ɗa'a)*"..

Bayan Allah ﷻ Ya faɗi wasu daga cikin siffofinsu a farkon Suratul-Anfal (kuma Ya tabbatar musu da cewa Ya yarda da ingancin imanin nasu kuma Ya karɓi ayukansu) sai Yace:

﴿ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ حَقّٗاۚ لَّهُمۡ دَرَجَٰتٌ عِندَ رَبِّهِمۡ وَمَغۡفِرَةٞ وَرِزۡقٞ كَرِيمٞ ٤ ﴾

"*Waɗannan su ne muminai na gaskiya. Suna da wasu darajoji (maɗaukaka) gun Ubangijinsu, tare da Gafara, da kuma wani irin (yalwataccen) arziki mai girma (daga Ubangiji Mai Karimci da Baiwa ga bayinSa nagari)*"..

Kamar yadda suke aikata duk abinda aka umurcesu na wajibai (har ma da nafilfilu), haka kuma suke matuƙar nisantar duk wata hanyar da za ta sa su afka cikin miyagun ayukan nan masu halakarwa.
A kullum suna matuƙar nisantan waɗannan manyan laifuka ne saboda **Tsoron Allah** da suke yi, da kuma fatan samun RahamarSa.

Allah ﷻ Ya yabe su akan hakan, kuma Ya tabbatar musu cewa wannan ɗin wata hanya ce ta samun GafararSa.
A cikin Suratun-Najmi (ayah ta **32**) Allah ﷻ Yace:

﴿ ٱلَّذِينَ يَجۡتَنِبُونَ كَبَٰٓئِرَ ٱلۡإِثۡمِ وَٱلۡفَوَٰحِشَ إِلَّا ٱللَّمَمَۚ إِنَّ رَبَّكَ وَٰسِعُ ٱلۡمَغۡفِرَةِۚ ٣٢ ﴾

"..*(Su ne) masu nisantar manyan laifuka (kaba'irai) da abubuwan alfasha (irin su zina da kuma miyagun kalamai), sai dai ƙananan laifuka (wannan kam zamiya tana kaisu ga aikatawa). Toh lallai Ubangijinka Mai yalwatacciyar Gafara ne*".

wannan gaɓa dai tana ƙara tabbatar wa masu imani ne cewa matuƙar sun nisanci waɗannan manyan laifuka, matuƙar sun tsare dokokin Allah sun ji tsoronSa, toh Zai gafarta musu zunubansu.

Ma'ana: Allah ﷻ Zai Gafarta musu laifukansu saboda inganta imaninsu da sukayi, da kyautata alaƙarsu daShi da sukayi ta hanyar aikata abinda Ya umurce su, da kuma nisantar manyan laifukan nan da Ya hanasu aikatawa.

Sanannen abu ne cewa Shirka ita ce mafi girma (mafi muni, kuma mafi haɗari) daga cikin waɗannan manyan laifuka[11].. Toh duk wanda ya nisanci shirka da sauran miyagun ayukan nan, kuma ya dage wajen yawaita ayuka nagari (tsakanin farillai da nafilfilu), Allah ﷻ (cikin FalalarSa da yalwatacciyar RahamarSa) Zai yafe masa sauran laifukan da ya aikata.

Allah ﷻ Ya yi alƙawarin hakan a cikin Suratun-Nisa'i (ayah ta: **31**) inda Yake cewa:

﴿ إِن تَجۡتَنِبُواْ كَبَآئِرَ مَا تُنۡهَوۡنَ عَنۡهُ نُكَفِّرۡ عَنكُمۡ سَيِّـَٔاتِكُمۡ وَنُدۡخِلۡكُم مُّدۡخَلٗا كَرِيمٗا ٣١ ﴾

"*Idan har kuka nisanci manyan laifukan (nan) da aka hane ku aikatawa (saboda Tsoron Allah); toh za Mu kankare muku munanan ayukanku, kuma za Mu shigar daku (wata irin babbar) mashiga ta karimci.*"

Sannan kuma Ya yi alƙawarin gafarta wa bayin nan naShi masu tsoron fakewa daga idanun mutane don su saɓa maSa, waɗanda suka fifita neman YardarSa akan ta mutane.

---

[11] Duba Saheehul-bukhari (hadithi na **2654**, da **6861**), Abu-Dawuda da Tirmidhi ma sun ruwaito shi..

A cikin Suratul-Mulk (aya ta 12) Allah ﷻ Yana cewa:

﴿ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَخۡشَوۡنَ رَبَّهُم بِٱلۡغَيۡبِ لَهُم مَّغۡفِرَةٞ وَأَجۡرٞ كَبِيرٞ ﴿١٢﴾ ﴾

*"Lallai waɗanda suke tsoron Ubangijin su a ɓoye (masu tsoron ɓuya su saɓa maSa, saboda yaƙinin da suke dashi akan lallai Yana ganinsu, kuma suna jin kunyarSa); toh suna da wata irin gafara (mai yawa) da kuma wani irin sakamako mai matuƙar girma (daga wajen Ubangijin nasu Maɗaukaki)."*

Ko shakka babu duk wanda ya doshi aikata wani aikin saɓo a ɓoye, sannan sai ya bar wannan aikin saboda ya tuna cewa ai Allah kam Yana ganinsa, wannan bawan Allah yana da imani mai ƙarfin gaske.

Shi yasa Allah ﷻ Yace duk mai irin wannan hali toh Ya yi masa alƙawarin Gafara da kuma lada mai yawa.

Allah ﷻ Ya ma ce Aljannah ce makomar duk mai irin wannan halin.
Haka Ya faɗa a can wajen ƙarshen suratun-Nazi'at (ayah ta 40-41) inda Yake cewa:

﴿ وَأَمَّا مَنۡ خَافَ مَقَامَ رَبِّهِۦ وَنَهَى ٱلنَّفۡسَ عَنِ ٱلۡهَوَىٰ ﴿٤٠﴾ فَإِنَّ ٱلۡجَنَّةَ هِيَ ٱلۡمَأۡوَىٰ ﴿٤١﴾ ﴾

"*Amma duk wanda yaji tsoron tsayuwa gaban Ubangijinsa (a gobe ƙiyama) sai ya hana kansa aikata abinda ransa yakeso (na laifi); toh lallai aljannah ita ce makoma (ga irin waɗannan bayin Allah masu imanin gaskiya)*"

Kuma Ya yi alkaƙwarin cewa in har bawa ya tsare dokokin Sa kuma Yaji tsoron sa a ko wanne hali, toh Zai datar da shi da daidai a cikin al'amuran sa na addini da rayuwa, kuma Zai gafarta masa zunuban sa.

Allah ﷻ Ya faɗi hakan ne a cikin Suratul-Anfal (ayah ta 29) inda Yake cewa:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِن تَتَّقُواْ ٱللَّهَ يَجۡعَل لَّكُمۡ فُرۡقَانٗا وَيُكَفِّرۡ عَنكُمۡ سَيِّـَٔاتِكُمۡ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡۗ وَٱللَّهُ ذُو ٱلۡفَضۡلِ ٱلۡعَظِيمِ ٢٩ ﴾

“*Ya ku waɗanda kukayi imani! In har kun tsare dokokin Allah (kunji tsoron Sa) toh Zai sanya muku mararraba*[12]*, Kuma Zai kankare muku ƙananan laifukan ku, kuma Zai Gafarta muku (manyan laifukan ku). Domin kuwa Allah Ma'abocin falala ne Mai Girma.*”

Da fatan Allah ﷻ Yasa da mu cikin masu tsoronSa a kowanne hali, kuma Yasa mu gama da duniya lafiya..

***

[12] mai rabewa tsakaninku da abinda kuke tsoron gamuwa da shi a duniya da lahira. Kuma Zai baku ilimi da basira Wacce za ku gane gaskiya daga ɓata. Kuma Zai datar da ku da abinda zai sa Ya yarda da ku a kullum.

## (Hanya ta Biyar)
## Biyayya ga Manzon Allah ﷺ,
## Da kuma nisantar saɓa masa

Bin Tafarkin Manzon Allah ﷺ, da yi masa biyayya a cikin komai na umurni da hani, da barin saɓa masa; wannan shi ne ma Musuluncin gaba ɗaya.
Shi ne tafarkin shiriya. Shi ne mafi girma daga cikin manyan alamomin imanin gaskiya.
Shi ne mafi ƙarfi daga cikin alamomin da suke nuna lallai da gaske bawa yana son Allah da manzonSa.
Shi ne mafi girma daga cikin hanyoyin da bawa zai bi don Allah ﷻ Yaso shi, kuma Ya yarda da shi.
Kuma yana daga cikin manyan hanyoyin samun Gafarar Allah ﷻ.

Za mu gane hakan ne idan muka duba cikin Suratu Ali-Imran (ayah ta **31** da ta **32**), inda Allah ﷻ Yake cewa:

﴿ قُلۡ إِن كُنتُمۡ تُحِبُّونَ ٱللَّهَ فَٱتَّبِعُونِي يُحۡبِبۡكُمُ ٱللَّهُ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡ ذُنُوبَكُمۡۚ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٣١ ﴾

"*Kace (musu): in har (da gaske) kun kasance kuna son Allah, toh ku bi ni. Shi kuma Allah Zai so ku (idan kukayi hakan), kuma Zai Gafarta muku zunuban ku. Domin kuwa Allah Mai yawan Gafara ne, kuma Mai Jinƙai*".

Wannan ayah dai tana nan ne a matsayin mizanin auna gaskiyar imanin duk wanda yace ya yarda da Allah ﷻ da ManzonSa ﷺ.

Allah ﷻ Ya sanya ɗa'a ga ManzonSa a matsayin sharaɗin ingancin imanin duk wanda yayi da'awar imani da Allah da ManzonSa.

Sannan Ya ƙara tabbatar da hakan a ayah ta gaba inda Yake cewa:

﴿ قُلْ أَطِيعُوا۟ ٱللَّهَ وَٱلرَّسُولَ ۖ فَإِن تَوَلَّوْا۟ فَإِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ ٱلْكَـٰفِرِينَ ﴿٣٢﴾ ﴾

"*Kace: kuyi ɗa'a (biyayya) ga Allah kuma kuyi ɗa'a ga Manzo (Muhammadu ﷺ). Amman suka juya baya (suka ƙi bin wannan umurni), toh fa lallai Allah ba Ya son kafirai.*"

Ko shakka babu lallai tsayuwa akan tafarkin Manzon Allah ﷺ da tsare masa haƙƙoƙinsa, da kyautata ladabi gareshi, da kuma nisantar saɓa masa: waɗannan su ne suke nuna lallai da gaske bawa ya yi imani da shi. Duk kuma wanda yayi hakan, Allah ﷻ Ya yi alƙawarin Zai Gafarta masa, kuma Zai bashi lada mai girma. Domin kuwa dole sai ya aikata su kafin ya samu tsira a duniya da lahira.
Shi yasa a farko-farkon Suratul-Hujurat (ayah ta **3**) Allah ﷻ Yake cewa:

﴿ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَغُضُّونَ أَصْوَٰتَهُمْ عِندَ رَسُولِ ٱللَّهِ أُو۟لَـٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ ٱمْتَحَنَ ٱللَّهُ قُلُوبَهُمْ لِلتَّقْوَىٰ ۚ لَهُم مَّغْفِرَةٌ وَأَجْرٌ عَظِيمٌ ﴿٣﴾ ﴾

"*Lallai waɗanda suke sassauta muryoyin su a wurin Manzon Allah ﷺ (saboda ladabin da suke masa), waɗannan su ne waɗanda Allah ﷻ Ya jarrabi zukatansu da taƙawa (kuma Ya datar dasu da cin wannan jarrabawa). Saboda haka suna da wata irin Gafara, da kuma lada mai girma (a wajen Allah ﷻ)*".

Tsira da Amincin Allah su ƙara tabbata ga wannan Manzo mai daraja, shi da iyalansa da Sahabbansa baki ɗaya, da kuma waɗanda suka biyo bayansu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako. Da fatan Allah Yasa har da mu cikinsu.

***

(Hanya ta Shida)

# Ayuka Nagari

Lallai ayuka na gari ma suna shafe munana, idan har bawa yayi sa'a yana da imani kuma ya nisanci shirka. Annabi ﷺ yana cewa: **"kaji tsoron Allah a duk inda kake. Ka riƙa bibiyan munanan ayukan ka da kyawawa, saboda su goge munanan. Kuma ka kyautata yadda kake mu'amala da mutane[13]."**

Wannan hadithi kuma shi yake ƙara fassara wannan magana ta Allah ﷻ inda Yake cewa:

﴿إِنَّ ٱلْحَسَنَٰتِ يُذْهِبْنَ ٱلسَّيِّـَٔاتِ ۚ﴾ [هود:١١٤]

"..*Lallai kyawawan ayuka suna tafiyar da munana*.."

Akwai misalai masu yawa daga cikin ayoyin Al-Kur'ani da kuma ingantattun hadithai da suke tabbatar da lallai ayuka nagari suna shafe munana (suna zama sanadiyyar samun gafarar Allah kan wasu laifukan da bawa ya aikata a baya)..

## A. Kyautata Tsarki da kuma cika Alwala, kamar yadda Manzon Allah ﷺ ya koyar

### KYAUTATA TSARKI

Haƙiƙa kyautata tsarki al'amari ne mai muhimmancin gaske a cikin addinin Musulunci. Tsarki dai sharaɗi ne daga cikin manyan sharuɗan karɓar duk wata Ibadar da bawa zai yi a rayuwarsa. Manzo ﷺ yace: **"Tsarki shi ne rabin imani[14]."**

Shi yasa Allah ﷻ Yake son duk wanda yayi ƙoƙari ya zama mai kyautata tsarkin sa.

---

[13] Tirmidhi ne ya ruwaito shi (hadithi na 1987) daga Sahabi Abu-dharrin Al-ghifari ﷺ

[14] Sahih-Muslim (hadithi na 223) daga Sahabi Abu-Maalik al-Ash'ariy

Har ma Ya yabi wasu bayinSa saboda hakan, inda Yake cewa:

﴿فِيهِ رِجَالٌ يُحِبُّونَ أَن يَتَطَهَّرُوا۟ۚ وَٱللَّهُ يُحِبُّ ٱلْمُطَّهِّرِينَ ﴿١٠٨﴾﴾ (التوبة: 108)

*"..A cikinsa (masallacin Kuba) akwai wasu mazaje (mutane) masu son suyi (kyakkyawan) tsarki, Allah kuma Yana son masu neman tsakakuwan nan*[15]*."*

Shi yasa ma aka umurce mu da neman Gafarar Allah a yayinda muka gama tsarki muka fito daga makewaya. Manzon Allah ﷺ ma ya kasance a duk lokacinda ya gama biyan buƙata ya fito, yana cewa:

غُفْرَانَكَ

"GafararKa nake nema[16] (Ya Allah)".

Ana neman Gafara yayinda aka fito daga makewaya saboda wasu dalilai.
Kaɗan daga cikinsu dai su ne kamar haka:

- Saboda a haɗa duk nau'ukan tsarkin biyu (najasar da aka kawar daga gangan jiki, da kuma dattin zunuban da ake da su)..
- Saboda bawa bai sani ba ƙila a yayin tsarkin nashi akwai wata najasar da ta fallatso masa a jiki (cikin rashin sani).

Duk da dai Allah ﷻ ba Ya kama bawa akan irin wannan (matuƙar dai babu sakaci), amma tare da hakan bawa yake neman Gafarar Allah ﷻ da RahamarSa.
Sannan kuma ya tabbata a sunnah lallai rashin kyautata tsarki yana cikin manyan laifukan da suke jawowa ayi wa bawa azaba a cikin ƙabarinsa[17].

---

[15] Suratut-Taubah (ayah ta **108**)

[16] Tirmidhi(**7**), Abu-Dawud(**30**), Ibnu-Majah(**300**).
Dukkan su daga **Uwarmu** (Nana) A'ishatu Allah Ya ƙaara mata Yarda da Daraja.

A wani hadithin ma, Manzon Allah ﷺ cewa yayi: **"Kuyi ƙoƙarin kuɓuta daga fitsari (ta hanyar kiyayewa sosai yayin da kuke tsarki) saboda yawancin azabar ƙabari daga (irin wannan) fitsarin ne[18]."**

Saboda haka aka umurci bawa da neman Gafarar Allah bayan ya fito daga makewaya, saboda ya samu kuɓuta daga wannan azabar.

Ashe tunda kuwa rashin kyautata tsarki yana da irin wannan muni, toh lallai wajibi ne mu kiyaye sosai. Musamman kuma ga shi mun gani cewa kyautata tsarkin yana daga cikin hanyoyin samun babban matsayi a wajen Allah ﷻ, kuma yana ma daga cikin hanyoyin samun gafarar Allah ﷻ. Da fatan Allah ﷻ Ya tsare mana imaninmu, Ya kuma ƙara tabbatar da mu akan karantarwar ManzonSa Annabi Muhammadu ﷺ har mutuwa.

## CIKA ALWALA

Yin alwala kamar yadda Manzon Allah ﷺ ya koyar, yana daga cikin muhimman hanyoyin samun Gafarar Allah Maɗaukaki. Kowa kuma zai samu wannan falala ne gwargwadon koyinsa da Manzon Allah ﷺ.

Akwai ingantattun hadithai masu yawa da sukayi bayani akan wannan al'amari. Ga kaɗan daga cikinsu insha'Allahu: Manzon Allah ﷺ yace: "**Duk wanda yayi alwala kuma ya kyautata alwalar, toh laifukan sa za su fice daga jikinsa -hatta ma waɗanda suke ƙarƙashin faratan sa**[19]".

Abin nufi: Duk wata gaɓar da aka wanke a yayin alwala, toh wannan ruwan alwala zai wanko har da zunuban da aka

---

[17] Bukhari (218), Muslim (212). Daga Sahabi abdullahi ɗan Abbas Allah Ya ƙara musu Yarda

[18] Ad-daara-ƙutniy ne ya ruwaito (hadithi na 464) daga Sahabi Abu-huraira ؓ

[19] Sahih Muslim (Hadithi na 245) daga Sayyiduna Usmanu ؓ.

aikata da wannan gaɓa, har bawa ya kasance tsaftatacce daga zunubai a yayinda ya kamala alwalar[20]"

Shi yasa aka kira alwala da sunan tsarki. Saboda bawa yana tsarkaka daga zunubansa ta hanyar kyautata alwala.

Wata rana[21] Manzon Allah ﷺ (ya tambayi Sahabbansa) yana cewa: "**Shin b azan nuna muku abubuwanda (ta dalilin aikata su) Allah ﷻ Zai share muku laifukan ku ba, kuma Ya ɗaga darajojin ku?**" Sai suka ce lallai muna so ka faɗa mana ya Manzon Allah. Sai yace: "**Cika alwala (kyautata shi) a daidai lokacinda ake ƙin taɓa ruwa[22], da kuma yawan tattaki zuwa wuraren sallah (masallatai), da kuma masu jiran sallah bayan wata sallar[23], Waɗannan lallai su masu ribaɗi ne. Lallai waɗannan su ne masu ribaɗi[24]**".
Manzon Allah ﷺ ya kamanta waɗannan ayuka guda uku da wannan babban al'amari na Jihadi, saboda girman aikin nasu a wajen Allah ﷻ.
Da fatan Allah ﷻ Yasa mu cikinsu.

Wata rana bayan Sayyiduna Usmanu ﷺ ya koya wa mutane irin alwalar Manzon Allah ﷺ, sai yace musu: Na ga Manzon Allah ﷺ

---

[20] Sahih Muslim (Hadithi na 244) daga Sahabi Abu-Hurairah ﷺ.

[21] Hadithin yana cikin Sahih Muslim (Hadithi na ) daga Sahabi Abu-hurairah ﷺ

[22] saboda yanayin da ake ciki na tsananin sanyi, yasa kowa yana jin nauyin amfani da ruwa sosai. Toh su duk da haka suna daurewa suyi alwala mai kyau

[23] Misali: Irin zaman nan da akeyi tsakanin Sallar Maghriba da isha'i, ko tsakanin Azahar da la'asar, ko kuma waɗanda suka shigo masallaci sukayi nafila suka zauna suna jiran lokacinda za a tayar da Iƙamar Sallar da take biye, da dai sauran makamantan su..

[24] Ribaɗi shi ne zaman daƙo cikin shiri da kimtsi (shirin ko ta kwana) saboda gabatar da wani aikin ibada don neman Yardar Allah. Aiki ne wanda dole sai an jure kafin a iya yin shi.
An kira waɗannan mutane uku masu ribaɗi ne, saboda irin himmar da suke da ita, da kuma tsantsar jajircewar su akan ibada.
Sannan kuma waɗanda aka fi sani da masu ribaɗi, su ne waɗanda suka zauna suka tare wushiryar yaƙi. Su ne waɗanda suka bar komai suka koma suka tare kafar da ake ganin maƙiya za su iya biyowa su farma al'ummah. Su ne Mujahidan nan da suka saida rayukan su don kare addinin Allah ﷻ. Da fatan Allah Yasa mu cikinsu.

ya yi irin wannan alwala, sannan sai yace: **Duk wanda yayi alwala kamar haka, za a gafarta masa abinda ya gabata na zunuban sa. Sannan tattakin da zaiyi zuwa Masallaci da kuma Sallar da zai yi a chan, su ma kuma wani irin ƙarin lada ne gareshi**[25]**”**

A wani lokacin kuma, shi Sayyiduna Usmanu ɗin yake cewa: “Lallai na ji Manzon Allah ﷺ yana cewa: **Babu wani mutum Musulmi da zai yi alwala kuma ya kyautata alwalarsa sannan kuma ya sallaci wata sallar, fahce sai Allah ﷻ Ya Gafarta masa abinda yake tsakanin wannan Sallah da kuma Sallar da take biye da ita**[26]”

## B. Sallah (ta farillah da ta Nafila)

Sallah ita ce mafi girma daga daga cikin dukkan rukunan Musulunci bayan Kalmar Shahada. Ita ce ma shaidar cewa mutum Musulmi ne. Daga cikin miliyoyin falalar ta marasa ƙidayuwa, Sallah tana cikin manyan hanyoyin samun Gafara. Idan har bawa ya kiyaye Sallar farillah, kuma ya dage da nafilfilu kamar yadda Manzon Allah ﷺ ya koyar, toh Allah ﷻ kuma Zai yafe masa zunubansa.
Babban misali akan wannan, shi ne faɗin Allah سُبْحَانَهُ وَتَعَالَىٰ (acikin Suratu Hud ayah ta 114) inda Yake cewa:

﴿ وَأَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَ طَرَفَيِ ٱلنَّهَارِ وَزُلَفًا مِّنَ ٱلَّيۡلِۚ إِنَّ ٱلۡحَسَنَٰتِ يُذۡهِبۡنَ ٱلسَّيِّـَٔاتِۚ ذَٰلِكَ ذِكۡرَىٰ لِلذَّٰكِرِينَ ١١٤ ﴾

“*Kuma ka tsaida Sallah a geffan nan biyu na yini da kuma wani yanki daga dare. Lallai kyawawan ayuka suna tafiyar da munana. Wannan fa tunatarwa ce ga masu (rabon) tunawa*”

Saboda amfanin da waɗannan sallolin guda biyar suke da shi ga bawa wajen tsaftace shi daga zunubai ne fa, yasa har

[25] Sahih Muslim (hadithi na 229) daga Sayyidina Usmanu ɗan Affan رضي الله عنه
[26] Sahih Muslim (hadithi na 227) Daga Sayyidina usmanu ɗan Affan رضي الله عنه

ma Manzon Allah ﷺ ya kamanta su da wanka sau biyar a yini.
Wata rana yace da Sahabbansa ﷺ: "**Shin baku gani ba; in har da ace akwai wata korama a ƙofar (gidan) ɗayanku, kuma a kowane yini yakan yi wanka aciki har sau biyar, shin akwai wani dattin da zai ragu a jikinsa ne? Toh haka ne misalin sallolin nan biyar. Allah ﷻ Yana share laifuka da su**[27] **(kamar yadda ruwan koramar nan yake wanke dattin jikin bawa)**".

Lallai ko shakka babu kiyaye Sallolin nan biyar, da kuma tattaki saboda halartarsu a cikin jama'a, da kuma zama a Masallaci saboda jiran Sallah; baki ɗaya waɗannan suna cikin muhimman hanyoyin samun Gafara.

Ya tabbata cewa idan ma bawa ya tashi ya kama hanyar zuwa Masallaci, toh gwargwadon takun da yayi da sawun sa shi ne yawan ladan da zai samu da kuma yawan zunuban da za a kankare masa. Domin kuwa Manzon Allah ﷺ yana cewa: "**Duk wanda yayi tsarki tun daga gidansa, sannan ya fito zuwa ɗaya daga cikin ɗakunan Allah saboda sauke wani farali daga cikin farillan Allah (Sallah), toh duk takun da yayi; ɗaya zai kankare masa laifi ne, ɗaya takun kuma zai ɗaga masa daraja**[28] ".

Ko shakka babu wannan wata falala ce mai yawan gaske da Allah ﷻ Yake wa bawanSa a yayin da ya kama hanyarsa ta zuwa Masallaci don gabatar da wata Sallah daga cikin Salloli.
Hakanan kuma duk wanda ya shigo Masallaci yayi Nafila sannan ya zauna yana jiran isowar Liman don a tada Sallah (da kuma wanda ya zauna bayan an idar da Sallah don jiran lokacin sallah ta gaba), su ma akwai wata irin falala mai

---

[27] Bukhari(**528**), Muslim (**667**) dukkansu daga sahabi Abu-Huraira ﷺ
[28] Sahih Muslim (hadithi na **666**) daga Sahabi Ubayyu ɗan Ka'ab ﷺ

yawa da Allah ﷻ Yake musu. Daga ciki dai, Mala'ikun Rahama za su nema musu gafara.
Manzon Allah ﷺ yace: "**Malaiku suna addu'a ga ɗayanku matuƙar yana zaune a inda yayi sallah kuma alwalarsa bata warware ba. Suna cewa (cikin addu'ar): Ya Allah Ka Gafarta masa, Ya Allah Kayi masa Rahama**[29]".

## Sallar Juma'a:

Manzon Allah ﷺ yace: "**Tsakanin Sallolin nan biyar (tsakanin kowacce sallah da ta gabanta), haka kuma tsakanin kowacce Juma'a da wata juma'ar; waɗannan dukka suna kankare zunuban da aka aikata tsakankaninsu, matuƙar dai an nisanci kaba'irai**[30]"

A wani hadithin ma, Manzo ﷺ cewa yayi: "**Duk wanda yayi wankan Juma'a, sannan ya taho Masallacin juma'a ya sallaci iya abinda aka ƙaddara masa (na nafilfilu kafin zuwan Liman), sannan ya zauna ya saurara har sai da Liman ya gama huɗubar sa, sannan yayi sallah tare da shi; toh za a Gafarta masa abinda yake tsakanin wannan juma'a da wata juma'ar, har ma da ƙarin wasu kwananki uku**[31]"

## Sallar Dare (Kiyamul-Laili, ko Tahajjudi)

Sallar dare (ko tsayuwar dare), Sallah ce ta nafila mai ɗumbin falala. Tana da lada mai yawa sosai. Lokacinta yana farawa ne tun daga bayan an gama sallar Isha'i har zuwa lokacin fitowar Alfijir. Mutum zai iya yinsa aduk lokacinda ya samu dama. Amma ingantattun hadisai sun tabbatar cewa yin wannan Sallah a ƙarshe-ƙarshen dare ya fi falala, ga wanda Allah ﷻ Ya baiwa ikon hakan.

---

[29] Bukhari: 445, Muslim: 649, dukkansu daga Sahabi Abi-Huraira ؓ
[30] Sahih-Muslim (hadithi na 233) daga Sahabi Abu-Huraira ؓ
[31] Sahih-Muslim (hadithi na 857) daga Sahabi Abu-Huraira ؓ

Wannan Sallah tana daga cikin ayukan Salihan bayin Allah. Domin kuwa Allah ﷻ Ya yabi masu yinta a cikin Al-Kur'ani mai girma a wurare daban-daban.
A cikin Suratu Ali-Imran (ayah ta 16 da 17) Allah ﷻ Yana cewa:

﴿ ٱلَّذِينَ يَقُولُونَ رَبَّنَآ إِنَّنَآ ءَامَنَّا فَٱغْفِرْ لَنَا ذُنُوبَنَا وَقِنَا عَذَابَ ٱلنَّارِ ﴿١٦﴾ ﴾

"*Sune waɗanda suke cewa: Ya Ubangijinmu hakika mu munyi imani, saboda haka (muna roƙonKa) Ka Gafarta mana zunubanmu, kuma Ka tsare mu daga azabar wuta*".

Sannan sai Ya cigaba da zayyana siffofinsu a cikin ayah ta gaba, inda Yake cewa:

﴿ ٱلصَّٰبِرِينَ وَٱلصَّٰدِقِينَ وَٱلْقَٰنِتِينَ وَٱلْمُنفِقِينَ وَٱلْمُسْتَغْفِرِينَ بِٱلْأَسْحَارِ ﴿١٧﴾ ﴾

"*Su (waɗannan bayin dai) su ne masu haƙuri kuma masu gaskiya (a kullum), su ne masu dagewa da Ibada, su ne masu ciyar da dukiyoyinsu (saboda neman Yardar Allah), su ne kuma masu neman Gafarar Allah a lokacinnan da ake kira "As-saharu" (wato lokacinda alfijir ya kusa fitowa)..*"

Hakanan ma acikin Suratuz-Zariyat (ayah ta 17 da ta 18), Allah ﷻ Yace:

﴿ كَانُوا۟ قَلِيلًا مِّنَ ٱلَّيْلِ مَا يَهْجَعُونَ ﴿١٧﴾ وَبِٱلْأَسْحَارِ هُمْ يَسْتَغْفِرُونَ ﴿١٨﴾ ﴾

"*Sun kasance basu yin bacci da dare sai ɗan kaɗan. Sannan a ƙarshen daren kuma, suna (dagewa da) neman Gafara*".

Akwai ingantattun hadisai masu yawa da suka tabbatar mana lallai wannan Sallah tana cikin manyan hayoyin Samun Gafara. Ga kaɗan daga cikinsu insha'Allah:

A cikin wani Hadithi mai ɗan tsawo[32] Manzon Allah ﷺ yace wa Sahabinsa Mu'azu ɗan Jabal ﵁: "**Shin ba zan nuna maka wasu ƙofofin alkhairi ba? Azumi garkuwa ce, ita ma sadaka tana kankare laifuka kamar yadda ruwa yake kashe wuta, haka ma sallar mutum a cikin dare take (tana da tasiri sosai wajen kankare zunuban bawa)**".
Sai kuma Manzo ﷺ ya karanta faɗin Allah ﷻ:

تَتَجَافَىٰ جُنُوبُهُمْ عَنِ الْمَضَاجِعِ يَدْعُونَ رَبَّهُمْ خَوْفًا وَطَمَعًا وَمِمَّا رَزَقْنَاهُمْ يُنفِقُونَ ﴿١٦﴾ فَلَا تَعْلَمُ
نَفْسٌ مَّا أُخْفِيَ لَهُم مِّن قُرَّةِ أَعْيُنٍ جَزَاءً بِمَا كَانُوا يَعْمَلُونَ ﴿١٧﴾ أَفَمَن كَانَ مُؤْمِنًا كَمَن كَانَ فَاسِقًا ۚ لَّا
يَسْتَوُونَ ﴿١٨﴾ أَمَّا الَّذِينَ آمَنُوا وَعَمِلُوا الصَّالِحَاتِ فَلَهُمْ جَنَّاتُ الْمَأْوَىٰ نُزُلًا بِمَا كَانُوا يَعْمَلُونَ ﴿١٩﴾

"*Gadajen bayansu suna nisantar makwantansu (a cikin dare), saboda suna can suna ta roƙon Ubangijinsu alhalin suna tsoronSa kuma suna kwaɗayin samun RahamarSa, sannan kuma (daga cikin ayukansu) suna ciyar da abinda Muka arzuƙta su. Babu wani rai da ta san irin abin jin daɗin da aka tanadar musu a ɓoye (a lahira), wanda sakamako ne gameda abinda suka kasance suna aikatawa (a duniya). Shin wanda ya kasance mai Imani, yana zama daidai da wanda ya kasance fasiƙi? Ba za su taɓa zama daidai ba. Amma su waɗanda sukayi imani kuma suka yi ayuka na ƙwarai, toh suna da (gidajen cikin) Aljannar tsira a matsayin masauki (na har abada) saboda abinda suka suka kasance suna aikatawa (na kyawawan ayuka a rayuwarsu ta duniya)*[33]"

Allah ﷻ Ya sanya wannan Sallah cikin manya-manyan alamomin salihan bayi. Ya kuma tabbatar musu da cewa lallai duk ibadar da sukeyi, Yana nan Yana adana musu, kuma a lahira Zai basu kyakkyawan sakamako.

Allah Yasa da mu cikinsu. Ameeen.

---

[32] Cikin Littafin Imam At-Tirmidhi (Hadithi na 2616) daga Sahabi Mu'azu ɗan Jabal ﵁
[33] Suratus-Sajdah (daga aya ta 16 zuwa ta 19)

Ita wannan Sallah fa a kowane dare ma idan akayi ta ana samun falala mai yawa, ballentana kuma in har Allah ﷻ Yasa muka iya raya dararen watan Ramadan kam, falalar tana da matuƙar yawa sosai da sosai fiye da sauran watanni.

Manzon Allah ﷺ yace: "Duk wanda yayi tsayuwar dare [34] a cikin Ramadan alhalin yana mai Imani kuma ya yi ne don neman lada a wajen Allah ﷻ, toh za a Gafarta masa abinda ya gabata na zunubansa[35]"

Haka kuma yace: "Duk wanda yayi tsayuwar dare a cikin daren Lailatul-ƙadari alhalin yana mai Imani, kuma yayi ne don neman lada; toh za a gafarta masa abinda ya gabata na zubanasa[36]"

Shi yasa lokacinda Matarsa mai daraja (kuma uwar muminai) Nana A'isha[37] ta tambaye shi addu'ar da za ta yi idan har Allah ﷻ Ya datar da ita da daren Lailatul-ƙadri, sai yace mata "Ki riƙa cewa:

اللَّهُمَّ إِنَّكَ عَفُوٌّ تُحِبُّ الْعَفْوَ فَاعْفُ عَنِّي

**"Ya Allah Lallai (Ka kasance) Kai Mai yafiya ne, kuma Kana son yafiya, saboda haka Ka yafe min**"

Manzon Allah ﷺ ya faɗa mata hakan ne, saboda babu abinda bawa yafi buƙata sama da Afuwar Allah da GafararSa da RahamarSa. Wannan kuma shi yafi komai ƙima cikin buƙatun bawa.

---

[34] Ana kiran ta Sallar Tarawih ko asham, ko Tahajjud, ko Kiyamul-laili, ko wutri, da dai sauran su.

[35] Bukhari 37, Muslim 759, dukkan su daga Sahabi Abu-Huraira ؓ

[36] Bukhari (35, 1901), Muslim (760), dukkan su daga Sahabi Abu-Huraira ؓ

[37] Allah Ya ƙaara mata Yarda

Toh a matsayinta na wacce yafi so kuma yafi ƙauna daga cikin matan duniya baki ɗaya, sai ya faɗa mata addu'ar da tafi dacewa ace ta yi a irin wannan lokacin. Saboda idan har Allah ﷻ Ya yiwa bawa Afuwa, toh Ya gama bashi Alkhairan duniya da lahira baki ɗaya.

Wannan dai kaɗan ne daga cikin irin ɗumbin falalar da ake samu idan har aka tsaida Sallah kuma aka dage da nafilfilun da suka tabbata a Sunnah.

Sai mu kyautata niyyah kuma mu dage sosai da sosai wajen ganin mun kyautata ibada a cikin ɗan lokacinda ya rage mana a rayuwa. Da fatan Allah Yasa mu dace da aikata abinda zai sama sanadiyyar samun RahamarSa garemu.

**C. Zakkah, da sadaka, da sauran hanyoyin taimako ga mabuƙata**

Daga cikin manya-manyan hanyoyin samun Gafarar Allah ﷻ, akwai fitar da Zakkah, bayar da Sadaka, da sauran hanyoyin taimakon mabuƙata, da kuma samar da 'yanci ga duk wanda yake cikin wani ƙangi[38].

## Zakkah:

Zakkah tana tsarkake dukiya. Kuma tana daga cikin alamomin ƙarfin imanin bawa. Sannan kuma hanya ce ta tsarkake bawa daga zunubai, saboda zai samu Gafarar Allah ﷻ idan ya fitar da ita kamar yadda aka umurce shi a shari'ance.

---

[38] Bauta, ko gidan yaari, ko kuma wani dabaibayi na ƙuncin rayuwa (musamman waɗanda aka zalunta)

A cikin Suratut-Taubah (ayah ta 103-104) Allah ﷻ Yace:

﴿ خُذۡ مِنۡ أَمۡوَٰلِهِمۡ صَدَقَةٗ تُطَهِّرُهُمۡ وَتُزَكِّيهِم بِهَا وَصَلِّ عَلَيۡهِمۡۖ إِنَّ صَلَوٰتَكَ سَكَنٞ لَّهُمۡۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ١٠٣ ﴾

"*Ka karɓi sadaka (zakka) daga cikin dukiyoyinsu don ka tsaftace su kuma ka tsarkake su da yin hakan, sannan kuma kayi musu addu'a (a yayinda suka fidda wannan zakkar), lallai addu'arka za ta zamto dalilin samun kwanciyar hankali garesu (a duniya da lahira), Shi kuma Allah ﷻ Shi ne Mai jin komai (daga cikin akwai roƙon bawa), Shi ne kuma Mai cikakkiyar masaniya akan komai (Ya san buƙatar kowa, kuma Ya san abinda ya dace da kowa cikin bayinSa)*".

Sannan sai Ya cigaba da cewa:

﴿ أَلَمۡ يَعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ هُوَ يَقۡبَلُ ٱلتَّوۡبَةَ عَنۡ عِبَادِهِۦ وَيَأۡخُذُ ٱلصَّدَقَٰتِ وَأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلتَّوَّابُ ٱلرَّحِيمُ ١٠٤ ﴾

"*Shin basu sani bane, cewa lallai Allah Shi ne (kaɗai) Mai karɓan tuban bayinSa, kuma Shi ne (kaɗai) Mai karɓan (ayukan da sukayi na bayarda) sadakoki (ga mabuƙata), kuma lallai Allah ﷻ Shi ne (kaɗai) Mai karɓar tuba (daga bayinSa), Shi ne kuma Mai Jinƙai?*"

## Sadaka:

Ita ma sadaka ɗaya ce daga cikin dalilai masu ƙarfi da suke nuna lallai bawa yana da gaskiya cikin imaninsa. Tana kuma yaye wa bawa fushin Ubangiji ﷻ, Saboda tana ɗaya daga cikin hanyoyin samun GafararSa.

Shi yasa Manzon Allah ﷺ yace: "**Ita ma sadaka tana kashe zunubai (tana kankare su) kamar yadda ruwa yake kashe wuta**[39]"

[39] Tirmidhi (hadithi na 2616) daga Sahabi Mu'azu ɗan Jabal ؓ

## Samar da ‘Yanci ga Bayin Allah, da kuma Kwatar Musu HakkinSu daga Hannun Azzalumai:

Duk wanda ya kyautata niyyah wajen ‘yanta wani Musulmi daga ƙangi na bauta (ko kuma ya ceto shi daga wani ƙunci na rayuwa); toh shi ma hakan zai zame masa sanadiyyar samun Gafarar Allah ﷻ. Domin kuwa Manzon Allah ﷺ yana cewa: “**Duk wani mutumin da ya ‘yanta wani mutum Musulmi, toh shi ma Allah ﷻ Zai ‘yanta kowacce gaɓa ta jikinshi daga wuta, da kwatankwacin irin wannan gaɓa ta jikin wanda ya ‘yanta ɗin**[40]”

Duk da dai a wannan zamani namu babu irin waɗannan bayin, amma wannan falalar dai tana nan. Domin kuwa yanzu haka a tsakankaninmu akwai waɗanda suke cikin wani irin ƙangi irin na masu bautan.
Wasu daga cikin mutanenmu (saboda rashin galihu) yanzu haka suna garƙame a cikin gidajen yari alhalin kuma babu laifin da sukayi.
Wasu kuma (saboda rashin mai tsaya musu) an nuna musu fin ƙarfi an ƙwace musu gida ko gona ko fili, da dai sauran nau’uka na cin zali iri-iri kamar yadda muke gani cikin gida da waje..

Toh idan har Allah ﷻ Ya baiwa mutum damar ƙwato wa irin waɗannan raunana haƙƙinsu daga hannun azzalumai, insha’Allahu zai samu irin wannan sakamakon da aka ambata acikin wannan hadithi mai daraja (matuƙar dai ya kyautata niyyah).
Allah Ya tsaremu daga zalunci da kuma sharrin azzalamai, Ya rufa mana asiri, kuma Yasa mu dace.

---

[40] Bukhari:2517, Muslim:1509, Abu-Dawud:2964, Tirmidhi:1547, Dukkansu daga Sahabi Abu-Huraira ﷺ

Lallai ne muyi amfani da duk wani abinda muka mallaka (na mulki da dukiya da ilimi da sauransu) wajen neman Yardar Allah ﷻ da kuma GafararSa da RahamarSa. Kada mu bari shaiɗan ya kai mu ya baro da ruɗe-ruɗen nan nashi marasa kan gado. Allah ﷻ Shi ne mai Alƙawarin Gaskiya, domin kuwa shi ne Ubangijin Gaskiya. Ya yi mana Alƙawarin cewa matuƙar mun bi umurninSa mun tsaya kan karantarwar AddininSa, kuma muka yi amfani da dukiyoyinmu kamar yadda Ya umurce mu; toh Zai Gafarta mana zunubanmu, kuma Zai bamu babban rabo a duniya da lahira. Acikin Suratul-Baƙarah (ayah ta 268) Allah ﷻ Yana cewa:

﴿ ٱلشَّيۡطَٰنُ يَعِدُكُمُ ٱلۡفَقۡرَ وَيَأۡمُرُكُم بِٱلۡفَحۡشَآءِۖ وَٱللَّهُ يَعِدُكُم مَّغۡفِرَةٗ مِّنۡهُ وَفَضۡلٗاۗ وَٱللَّهُ وَٰسِعٌ عَلِيمٞ ٢٦٨ ﴾

"*Shaiɗan yana (ruɗar ku kuma yana tsorata ku ta hanyar) yi muku alƙawari da talauci (in har kuka ciyar da dukiyoyin ku akan neman yardar Allah), kuma yana umurtan ku da alfasha (wato yana so kuyi amfani da dukiyoyinku akan saɓon Allah). Shi kuma Allah Yana muku alƙawarin Gafara daga gareShi da kuma wata irin babbar falala (in har kuka yi miShi biyayya kuma kuka saɓa wa shaiɗan), domin kuwa Allah Mawadaci ne kuma Masani*"..

Allah Ya bamu arziki mai Albarka, wanda zai zama sanadiyyar samun babban rabo garemu a duniya da lahira.

## D. Azumi (na farillah da na nafilah)

Azumi wani irin sirri ne tsakanin bawa da Ubangijinsa. Wata Ibada ce wacce babu wanda yasan yawan ladan ta sai Allah ﷻ.

Azumi Yana daga cikin manyan hanyoyin shiga Gidan Rahama. Akwai ƙofa ma ta musamman a Aljannah da aka tanadar da ita don masu azumi kaɗai. Idan suka shige za a kulle ƙofar, babu mai ƙara biyowa ta nan kuma har abada.

Sannan kuma Azumi yana daga cikin manya-manyan hanyoyin samun Gafarar Allah ﷻ. Shi yasa ma aka sanya shi acikin jerin galibin nau'ukan kaffarah da aka ɗora wa bawa idan ya aikata wasu manyan laifuka. Kaɗan daga cikinsu su ne kamar haka:

- Wanda yayi kisan kai a bisa kuskure, akwai diyyah akansa, da kuma azumin wata biyu (kwana sittin kenan).
- Wanda yayi rantsuwa akan abu, sannan sai daga baya ya karya wannan rantsuwar, cikin nau'ukan kaffararsa akwai azumi uku.
- Wanda yayi zihari (wato ya kamanta saduwa da matarsa ta sunnah da kwanciya da mahaifiyarsa), sannan daga baya ya koma ga matar; toh dole sai ya yi kaffarah kafin ta halatta gareshi. Daga cikin jerin nau'ukan kaffarar kuma, akwai azumi sittin.
- Wanda ya sadu da iyalinsa da rana alhalin kuma da azumin Ramadan a bakinsa, shi ma dole sai ya yi kaffarah. Daga cikin jerin nau'ukan kaffarar kuma akwai azumin wata biyu.
- Wanda yayi wani laifi a cikin aikin hajji, irin laifin da aka ɗora masa hukuncin nan da ake kira fidiya, toh (matuƙar ba mazaunin garin Makka ba ne shi) dole sai ya yi wannan kaffarah. Daga cikin nau'ukan kaffarar kuma akwai azumi goma (uku a harami, bakwai kuma idan ya koma gida).

..Da dai sauran su..

An saka azumi a cikin waɗannan nau'ukan kaffarah ne, saboda irin muhimmancin da azumin yake da shi wajen kankare zunuban mutum. Da fatan Allah ﷻ Yasa mu cikin bayinSa masu himma wajen azumi (na farilla da nafila), kuma Ya gafarta mana zunubanmu, Yayi mana Afuwa, Ya kuma Yi mana Rahama.

## Azumin Ramadan:

Manzon Allah ﷺ yana cewa: "**Duk wanda ya azumci Ramadan alhalin yana mai imani, kuma yayi hakan ne don neman lada a wajen Allah ﷻ; toh za a Gafarta masa abinda ya gabata na zunubansa**[41]"

## Azumin Nafila:

Kamar yadda azumin Farillah yake da falala mai yawa, haka ma azumin nafila yake. Domin kuwa Manzon ﷺ ya kwaɗaitar sosai akan yin azumin nafila, saboda ɗumbin falalar da hakan yake da ita.

Tabbas azumi yana da lada mai yawa sosai, kuma yana daga cikin manyan hanyoyin samun Gafarar Allah ﷻ.

Daga cikinsu akwai azumin ranar Arafah (**9** ga watan zulhajji, ranar jajiberen babbar sallah), da kuma ranar Ashura (wato **10** ga watan Al-Muharram)..

Sahabi Abu Katadah ؓ yana cewa: "Wata rana an tambayi Manzon Allah ﷺ gameda falalar azumtar ranar Arafah, sai yace: **Tana kankare zunuban shekaru biyu, wacce ta gabata da kuma wacce take biye**. Sannan da aka tambayeshi gameda falalar azumtar ranar ashura' kuma, sai yace: **Tana kankare zunuban shekara guda, wacce ta gabata**[42]"

## E. Aikin Hajji da Umrah:

[41] Bukhari (38, 1901), Muslim (760) Daga Sahabi Abu-huraira ؓ

[42] Sahih Muslim (Hadithi na 1162)

Aikin Hajji da Umrah ma suna daga cikin manyan hanyoyin samun Gafara. A cikin Suratul-Baƙarah bayan Allah ﷻ Ya yi bayanin wasu dokoki na aikin Hajji, sai Yace[43]:

﴿ ثُمَّ أَفِيضُواْ مِنْ حَيْثُ أَفَاضَ ٱلنَّاسُ وَٱسْتَغْفِرُواْ ٱللَّهَۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ١٩٩ ﴾

"*Sannan sai ku kwararo ta inda sauran mutane suka kwararo (ku gangaro tare da sauran mutane daga farfajiyar Arafah zuwa Muzdalifa, can bayan faɗuwar rana), kuma ku nemi Gafarar Allah ﷻ, Saboda lallai Shi Allah ﷻ Mai yawan Gafara ne, kuma Shi Mai yawan Jinƙai ne*"

Manzon Allah ﷺ kuma yace: "**duk wanda yayi aikin hajji alhalin bai yi wani rafathu**[44] **ba, kuma bai yi wani aiki na fasiƙanci ba (a yayin wannan aikin hajji nashi) har ya gama; toh zai dawo (gida) kamar ranar da mahaifiyarshi ta haife shi**[45]"

Abin nufi: Allah ﷻ Zai yafe masa baki ɗaya laifukan sa, har ya zama kamar bai taɓa aikata wani laifi ba a rayuwarsa.

A cikin wani hadisin kuma, Manzo ﷺ yace: "**Daga wata Umrah zuwa wata Umrar (ta daban), ana kankare zunuban da aka aikata tsakaninsu. Shi kuma Hajji karɓaɓɓe, bai da wani sakamako sai Aljannah**[46]"

**Allahu Akbar**

---

[43] Acikin ayah ta 199
[44] Saduwa da iyali, da duk abinda ya danganci hakan
[45] Bukhari:1521, Muslim:1350, daga Sahabi Abu-Huraira رضي الله عنه
[46] Bukhari:1773, Muslim:1349

## F. Karantar da mutane addinin Allah, da sanar da su hanyoyin alheri

Daga cikin hanyoyin samun Yardar Allah da GafararSa da RahmarSa; akwai karantar da mutane Addini, da sanar da su hanyoyin Alkhairi, da umurtansu da kyawawan aiyuka, da kuma hana su munana, da ƙyamatar da su aikata dukkan wani aiki na saɓo, da kuma nuna musu Girman Allah don su ji tsoronSa kuma su tsare dokokinSa..

A cikin Suratut-Taubah (ayah ta 112) Allah ﷻ Ya lissafa masu irin wannan aiki daga cikin bayinSa na ƙwarai masu babban rabo a duniya da lahira, waɗanda Yayi musu bishara saboda Yarda da Yayi da imaninsu. Yace:

﴿ٱلتَّٰٓئِبُونَ ٱلۡعَٰبِدُونَ ٱلۡحَٰمِدُونَ ٱلسَّٰٓئِحُونَ ٱلرَّٰكِعُونَ ٱلسَّٰجِدُونَ ٱلۡأٓمِرُونَ

بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَٱلنَّاهُونَ عَنِ ٱلۡمُنكَرِ وَٱلۡحَٰفِظُونَ لِحُدُودِ ٱللَّهِۗ وَبَشِّرِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ١١٢﴾

"*Su ne masu Tuba, masu kyautata bautarsu, masu yawan godiya, masu yin tafiye-tafiye don ayukan ɗa'a (irinsu aikin hajji, jigadi, ziyara, duba mara lafiya da dai sauransu), su ne masu umurni da kyawawan ayuka kuma suke hana munana, su ne masu tsare dokokin Allah. Saboda haka kayi Albishir ga (irin waɗannan bayi) masu imani (an karɓi ayukansu kuma an yafe musu zunubansu)*".

Manzo ﷺ yace: "**Lallai shi Malami**[47]**, duk waɗanda suke cikin sammai da ƙassai suna nema masa Gafarar Allah, hatta kifaye acikin ruwa (su da sauran halittun ruwa baki ɗayansu suna nema masa Gafara wajen Allah ﷻ)**[48]"

[47] Mai karantar da al'ummah da ikhlasi, kuma ya tsaya kan karantarwar Manzon Allah ﷺ

[48] Abu-Dawud (hadithi na 3641), Tirmidhi (hadithi na 2682) daga Sahabi Abud-Dardaa'i ؓ. Hadisin ya inganta. Duba Saheeh_Sunan_Abi-Dawud hadithi na 3096

Duk halittun nan da suke cikin sammai da ƙassai suna nema wa malami Gafara dare da rana, ta hanyoyin da babu wanda yasan ma adadinsu sai Allah ﷻ.

Bayan haka kuma, shi ma yana ta tara lada mai yawan gaske (saboda yana da ladan duk wani harafi guda ɗaya da ya koya wa mutane, sannan kuma duk lokacinda akayi aiki da wannan ilimin da ya koyar -ko da kuwa bayan nutuwarsa ne- sai shi ma an bashi kwatankwacin irin ladan da aka baiwa masu aikin, ba tare da kuma an tauyewa kowa komai ba).
Ko shakka babu wannan falala ce babba sosai. Babu wanda ya cancance ta sai Malamai magada Annabawa.
Allah Ya saka wa Malamanmu (na da da na yanzu dukka) da Alkhairi, Ya Gafarta musu zunubansu, Ya kankare musu kurakuransu, Ya ƙara wa iliminsu Albarka, Ya ƙara kare mana su daga duk wani sharri, da irin kariyar da Yake wa manyan bayinSa (a duniya da lahira).

Ya mai karatu! Lallai dole ne mu tashi mu nemi ilimin addinin Allah ﷻ, don sanin yadda zamu bauta maSa kamar yadda Yai umurni. Dole mu tashi muyi karatu, don mu kawar wa kawunanmu jahilci, mu kuma kawar wa sauran Al-ummar da muke rayuwa tare (ta hanyar karantar dasu addinin gaskiya).
Laifi ne babba a zauna kara zube ba a karatun addini. Hakan yana da mummunan haɗari garemu cikin addininmu da rayuwarmu baki ɗaya. Domin kuwa idan jahilci ya kanannaɗe al-ummah, toh babu irin taɓarazar da ba za a gani ba.
Zama cikin jahilci zai sa a koma ana rayuwa irin ta dabbobi, domin kuwa babu irin ɓarnar da ba za a fito fili ana aikatawa ba.

Babu kuma wata al'ummar da ta cigaba cikin jahilci. Kuma baki ɗaya Annabawa da Manzanni da Salihan bayi dukkansu sun nemi tsari daga jahilci.

Sannan su ma waɗanda Allah ﷻ Ya zaɓe su Ya sanar dasu wani abu na ilimi, toh fa wajibi ne akansu suyi aiki da shi. Domin kuwa duk wanda ya sani kuma ya take, toh laifinsa babba ne a wurin Allah ﷻ. Bal ma azabarsa daban ce acikin wuta. Saboda tsananin azabar da za ayi masa ma, har wasu daga cikin 'yan wutan za su taru suna kallon yadda ake masa (tare da su ma ɗin suna cikin wutar).
Haka Manzon Allah ﷺ yace. Hdisin yana nan cikin Sahihul-Bukhari[49] inda yake cewa: "**Za a taho da wani mutum a jefar da shi cikin wuta. Za a ɗaure shi (da hanjinsa) kamar yadda ake ɗaure jaki a jikin tirkensa (da igiya). Har sauran 'yan wuta su kewaye shi (suna kallon irin azabar da ake masa), su riƙa ce masa ya kai malam wane, ba kai ne (a duniya) ka kasance kana umurni da kyawawan ayuka kuma kana hani da munana ba? Sai yace musu:**

إِنِّي كُنْتُ آمُرُ بِالْمَعْرُوفِ وَلاَ أَفْعَلُهُ، وَأَنْهَى عَنِ الْمُنْكَرِ وَأَفْعَلُهُ

Zai ce (can a bakinsa): '**Lallai (hakane) ni na kasance ina umurni da kyawawan ayuka amma ni ba na aikatawa. Ina kuma hani da munana amma ni ina aikatawa (a ɓoye)**".
Wasu hadithai ma sun tabbatar cewa da irin waɗannan shaiɗanun malamai za a fara hura wutar jahanna a gobe Kiyamah.

---

[49] Hdithn Sahabi Usaamah ɗan Zaid Allah Ya ƙara musu Yarda (shi da mahaifin nashi dukka). Yana ma cikin Sahih Muslim

Shi yasa ma wani mawaƙi (acikin wasu baitocinsa) yake cewa:

وَعالِمٌ بِعِلْمِهِ لا يَعْمَلَنْ # مُعَذَّبٌ قَبْلَ عُبَّادِ الْوَثَنِ

"Kuma duk Malamaninda baya aiki da iliminsa, toh lallai shi za a fara yiwa azaba (a wuta) kafin ma ayiwa masu bautan gumaka."

Haka nan rowar ilimi ma babban laifi ne sosai. Saboda Manzon Allah ﷺ yana cewa: "**Duk wanda aka tambaye shi wani ilimi sai ya ɓoye shi (ya ƙi ya sanar da mutane), toh za a sanya masa linzamin wuta a ranar Kiyamah**[50]"

Su fa masu umurni da kyawawan ayuka kuma suke hana munana, a kullum cikin nasara suke a rayuwarsu (ta duniya da lahira). Domin kuwa bayan ɗumbin ladan da suke samu ta fiskoki daban daban, da kuma zunubansu da ake ta kankare musu a kullum, har ila yau kuma su (da waɗanda suka amsa kiransu) ne kaɗai suke tsira a duk lokacinda wata uƙuba ta sauka ga kangararrun bayi. Allah ﷻ Yana tserar da su ne saboda wannan babban aikin da suka tsaya sukayi ta yi na gadon Annabta. Allah ﷻ Ya bamu labarin yadda Yayi ta tserar da Annabawa da Manzanni masu yawa a cikin Al-Kur'ani mai girma, su da waɗanda sukayi imani dasu cikin al'ummomin su. Haka kuma Ya ma bamu labarin yadda Ya tserar da wasu Malamai masu faɗakar da al'umma, su da waɗanda suka amsa kiran su.

---

[50] Abu-Dawud (3658), Tirmidhi (2649). Hadithi ne ingantacce, duba Sahih_sunan_Abi-Dawud (3106)

Misali a cikin suratul-A'rafi (ayah ta **164** zuwa ta **166**) Allah ﷻ Yana cewa:

﴿وَإِذْ قَالَتْ أُمَّةٌ مِّنْهُمْ لِمَ تَعِظُونَ قَوْمًا ٱللَّهُ مُهْلِكُهُمْ أَوْ مُعَذِّبُهُمْ عَذَابًا شَدِيدًا ۖ قَالُوا۟ مَعْذِرَةً إِلَىٰ رَبِّكُمْ وَلَعَلَّهُمْ يَتَّقُونَ﴾

"*Kuma a lokacinda wasu mutane (marasa gaskiya) daga cikinsu suka ce (wa masu wa'azi): wai shin me yasa kuke ta yin wa'azi ga mutanenda tabbas Allah Zai halaka su, ko kuma Yayi musu azaba mai tsanani? Sai (su masu wa'azin) suka ce: muna hakan ne domin neman hanzari zuwa ga Ubangijinku (saboda kar Ya kama mu da laifin rashin wa'azi ga maɓarnata), da kuma tsammanin (wasu daga cikinsu) za su (wa'aztu) suyi taƙawa (su daina ayukan saɓon da sukeyi)*".

Wannan akullum itace gwagwarmayar da take tsakanin Malamai nagari (masu neman Yardar Allah) da kuma miyagun malamai (waziran shaiɗan daga cikin mutane). Acikin ayah ta gaba kuma sai Allah ﷻ Yace:

﴿فَلَمَّا نَسُوا۟ مَا ذُكِّرُوا۟ بِهِۦٓ أَنجَيْنَا ٱلَّذِينَ يَنْهَوْنَ عَنِ ٱلسُّوٓءِ وَأَخَذْنَا ٱلَّذِينَ ظَلَمُوا۟ بِعَذَابٍۭ بَـِٔيسٍۭ بِمَا كَانُوا۟ يَفْسُقُونَ ١٦٥﴾

"*Toh a lokacinda suka manta da abinda aka tunatar da su (suka ƙi aiki da shi), Mun tserar da waɗanda suke hani da munanan ayuka, kuma Muka kama waɗanda sukayi zalunci da azaba mai matuƙar tsanani, domin abinda suka kasance sunayi na fasiƙanci*".

Sannan a gaba kuma sai Yace:

﴿ فَلَمَّا عَتَوْا۟ عَن مَّا نُهُوا۟ عَنْهُ قُلْنَا لَهُمْ كُونُوا۟ قِرَدَةً خَـٰسِـِٔينَ ﴿١٦٦﴾ ﴾

"*Sa'nnan a lokacinda suka yi girman kai suka ƙi barin abinda aka hanesu aikatawa, sai muka ce musu Ku kasance birrai ƙasƙantattu (Muka mayar da su birai, sukayi ta rayuwa cikin ƙasƙanci da wulakanci)*".

Wannan yake tabbatar da cewa lallai babu mai tsira a duniya da lahira sai wanda ya tsaya kan Tafarkin Manzon Allah ﷺ. Idan aka duba ayah ta 52 cikin Suratun-Nur, Allah ﷻ Yana cewa:

﴿ وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَيَخْشَ ٱللَّهَ وَيَتَّقْهِ فَأُو۟لَـٰٓئِكَ هُمُ ٱلْفَآئِزُونَ ﴿٥٢﴾ ﴾

"*Kuma duk wanda yayi ɗa'a ga Allah da ManzonSa, kuma ya ji tsoron Allah kuma ya tsare dokokinSa, to waɗannan su ne masu babban rabo*"

Toh malami mai gaskiya cikin imaninsa shi ne wanda zai kyautata niyyah tsakaninsa da Allah, kuma yake bin tafarkin Manzon Allah ﷺ wajen isar da saƙon Allah ga bayinSa. Rashin bin wannan tafarki yana da haɗari sosai.
Domin kuwa Manzon Allah ﷺ yana cewa: "**Na rantse da wanda rayuwa ta take HannunSa! Dole (ku tashi) kuyi umurni da kyakkyawan aiki, kuma dole kuyi hani da mummuna. In ba haka ba kuma, toh za a kai wani yanayinda Allah ﷻ (Zai yi fushi) Ya saukar muku da uƙuba daga gareShi, kuma (a irin lokacin nan) ko kun roƙe Shi (don Ya yaye muku) ma, ba Zai amsa muku roƙon naku ba**[51] **(saboda baku cika sharaɗin karɓar addu'ah ba)**".

[51] Tirmidhi (hadithi na 2169) daga Sahabi Huzaifah al-Yamaani ؓ

## G. Biyyaya ga iyaye, kyautata musu, da kuma barin saɓa musu ko cutar da su

Daga cikin manyan hanyoyin samun gafarar Allah ﷻ; akwai kyautata wa iyaye, da kuma nisantar saɓa musu. Domin kuwa **Yardar Allah tana cikin yardar iyaye, haka ma FushinSa yana cikin fushinsu**[52].
Bayan haƙƙin Allah ﷻ da na Manzo ﷺ babu haƙƙin da yakai na iyaye. Shi yasa acikin ayoyi masu yawa ma ake yawaita kawo batun kyautatwa iyaye da zarar an gama umurni da kaɗaita Allah da bauta.
Saboda haka duk mai son gamawa da duniya lafiya; toh fa dole ne ya sasanta da iyayen shi ya zauna lafiya da su, kuma ya riƙa kyautata musu. Sannan kuma dole ne ya guji saɓa musu akan duk abinda ba saɓon Allah ba ne. Kar kuma ya yarda ya cutar da su ko ta wane hali ne. Saɓa wa iyaye laifi ne mai matuƙar girma. Kuma tun daga nan duniya bawa zai fara ɗanɗana uƙuba kafin yaje lahira ya tarar da sakamakon mummunan aikinsa.

Lallai ne duk wani ɗa nagari yayi ƙoƙarin ganin ya nemi Aljannah ta hanyar kyautata wa iyayensa.
Manzon Allah ﷺ yana cewa: "**Allah Ya turbuɗe hancin duk wanda ya riski tsufan mahaifansa –sawa'un ɗaya daga cikinsu ne ko su biyun dukka- kuma (har suka mutu) bai yi musu wani abin kyautatawan da zai zama sanadiyyar shigarsa Aljannah ba**[53]**. Allah Ya turbuɗe hancinsa (ma'ana: Allah wadaransa. Domin kuwa ba zai taɓa samun dacewa ba a rayuwa)**."

---

[52] Tirmizi (Had1si na 899) daga Sahabi Abdullahi ɗan 'Amru ɗan Aas (Allah Ya ƙara musu Yarda su biyun duka).
[53] Sahih Muslim (hadisi na 2551) daga Sahabi Abu.-Huraira ؓ.

A cikin wannan hadisi za mu ga ashe biyayya ga iyaye (da kuma kyautata musu) yana daga cikin hanyoyin samun Gafarar Allah ﷻ. Sannan rashin kyautata musu kuma, yana daga cikin ababenda suke cire albarka a rayuwar bawa. Allah Ya tsare mana imaninmu. Sannan kuma akwai hadisan da suke ƙara tabbatar da lallai Allah ﷻ Yana tserar da irin waɗannan (masu kyautatawa iyayensu) daga faɗawa cikin wani haɗari ko bala'i, sakamakon biyayyar da suke wa iyayensu.

Za mu ga misalin hakan a cikin hadithin da Manzon Allah ﷺ ya bada labarin wasu mutane su uku da suka shiga cikin wani ƙogo suka fake, sai wani ƙaton dutse ya gangaro ya rufe ƙofar ƙogon alhalin suna ciki (ga shi kuma acikin ƙungurmin daji ne mai nisa, saboda haka babu mutane kusa ballentana su taimake su).
Saboda haka sai suka yanke shawara akan lallai ne kowanne daga cikinsu yayi tawassuli da wani aikinsa nagari (wanda yake fatan Allah ﷻ Ya karɓa masa) wajen roƙon Allah ﷻ don Ya kuɓutar dasu daga wannan halakar da suke gani ido da ido.
Sun roƙi Allah ﷻ kuma Ya amsa musu. Domin kuwa Ya kuɓutar dasu daga wannan ramin da suke binne a ciki da rayukansu.
Toh daga cikinsu akwai wanda yayi tawassuli da biyayyar da yayi wa mahaifan sa (waɗanda sun riga sun tsufa) da kuma kyautata musu da yayi, tare da fifita su akan akan iyalansa (mata da kuma yara ƙanana)[54].

[54] Bukhari (2272), Muslim (2743), daga Sahabi Abdullahi ɗan Umar, Allah ƙara musu yarda.

## H. Yiwa mutane Afuwa:

Yafewa mutane abinda suka sukayi na laifi ko kuskure (da kuma rangwanta musu), wannan babban lamari ne wanda sai masu babban rabo awajen Allah ﷻ suke iyawa. Shi Yasa Allah ﷻ Ya lissafa wannan aiki cikin halayen manayan bayinSa. Misali ɗaya gameda hakan shi ne inda Yake cewa:

﴿ وَإِذَا مَا غَضِبُواْ هُمۡ يَغۡفِرُونَ ٣٧ ﴾ [الشورى:٣٧]

"..*Kuma idan ma sukayi fushi (ma'ana idan aka ɓata musu rai ta) sai kaga suna yin gafara*"

Kenan hakan ya nuna duk mai yafewa wani, toh shi ma Allah ﷾ Zai yafe masa. Acikin Suratun-Nur (ayah ta 22) Allah ﷻ Yana cewa:

﴿ وَلۡيَعۡفُواْ وَلۡيَصۡفَحُوٓاْۗ أَلَا تُحِبُّونَ أَن يَغۡفِرَ ٱللَّهُ لَكُمۡۚ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٌ ﴾ [النور:٢٢]

"Kuma suyi afuwa su ƙyale (kar su ɗauki wani mataki na ramako akan wanda ya cutarda su). Shin ku baku so Allah ﷻ Ya Gafarta muku ne? Alhalin kuma Allah ﷻ Shi ne Mai Yawan Gafara kuma Shi ne Mai jinƙai!!"

Ka ga ashe hakan yana cikin hanyoyin samun Gafarar Allah ﷻ. Kuma Yana cikin hanyoyin samun Soyayyar Allah ﷻ ga bawa. Shi Yasa acikin Suratu Ali-Imran (ayah ta **134** zuwa **136**) Allah ﷻ Yake cewa:

﴿ ٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ فِي ٱلسَّرَّآءِ وَٱلضَّرَّآءِ وَٱلۡكَٰظِمِينَ ٱلۡغَيۡظَ وَٱلۡعَافِينَ عَنِ ٱلنَّاسِۗ وَٱللَّهُ يُحِبُّ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ١٣٤ ﴾

*"Su ne waɗanda suke ciyarda dukiyoyinsu (a kullum) sawa'un ana cikin walwala ne ko ana cikin ƙunci, suna haɗiye fushinsu, suna yafewa mutane, lallai Allah Yana son (waɗannan bayi nagari) masu kyautatwa*".

﴿ وَٱلَّذِينَ إِذَا فَعَلُواْ فَٰحِشَةً أَوۡ ظَلَمُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ ذَكَرُواْ ٱللَّهَ فَٱسۡتَغۡفَرُواْ لِذُنُوبِهِمۡ وَمَن يَغۡفِرُ ٱلذُّنُوبَ إِلَّا ٱللَّهُ وَلَمۡ يُصِرُّواْ عَلَىٰ مَا فَعَلُواْ وَهُمۡ يَعۡلَمُونَ ١٣٥ ﴾

"*Kuma su ne dai waɗanda idan suka aikata wani laifi ko suka zalunci kawunansu (ta hanyar saɓawa Allah ﷻ) toh nan take suke tuna Allah su nemi GafararSa gameda zunubansu, saboda babu mai Gafarar zunubai sai Allah ﷻ, sannan (bayan haka) basu dogewa su kafe akan abinda suka aikata (na munanan ayuka) alhalin suna sane (suna gaggauta barin aikin, suyi nadama akansa, su nemi Gafara Allah, sannan kuma su ƙauracewa duk abinda zai iya kusanto da su zuwa ga wannan mummunan aiki, ballenta su kuma aikata shi nan gaba)*".

﴿ أُوْلَٰٓئِكَ جَزَآؤُهُم مَّغۡفِرَةٞ مِّن رَّبِّهِمۡ وَجَنَّٰتٞ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَاۚ وَنِعۡمَ أَجۡرُ ٱلۡعَٰمِلِينَ ١٣٦ ﴾

"*Irin waɗannan suna da sakamakon wata irin Gafara daga Ubangijinsu, da kuma Aljannatai waɗanda koramu (na dangin ababen sa daban daban) suke gudana a ƙarƙashinsu, za su dawwama a ciki, Madallah da (irin wannan) lada (wanda yake a matsayin sakamako) ga waɗannan ma'aikata*"

Ko shakka babu masu yiwa mutane afwa su ma Allah ﷻ Zai yafe musu. Saboda haka duk wanda yake kyautata niyyah ya tausaya wa wani, toh shi ma Allah ﷻ Zai tausaya masa. Domin kuwa Allah ﷻ Yana jinƙan bayinSa masu jinƙai. Shi yasa ma hatta mutumin da yake sassauta wa bayin Allah a cikin kasuwancinsa, kuma ba ya tsawwala musu, toh shi ma Allah ﷻ Zai masa afuwa a duniya da lahira (matuƙar ya mutu ba ya shirka). Allah ﷻ Zai ƙara wa dukiyarsa albarka, Zai rufa masa asiri, kuma Zai kare shi daga uƙuba.

Manzon Allah ﷺ yace: "**Akwai wani (ɗan kasuwa) mutumin kirki wanda ya kasance yana baiwa mutane bashi. A kulumm yana cewa kowa daga cikin yaran gidansa idan ka je gun wani (daga cikin waɗanda muke bi bashi) amma ka riske shi cikin tsananin rashi, toh kayafe masa kawai (ka cire sunan shi daga cikin jerin waɗanda muke binsu bashi), da fatan mu ma (a gobe Kiyama) Allah Allah ﷻ Zai Yafe mana (a daidai lokacinda muka fi matuƙar buƙatar RangwamenSa da GafararSa da RahamarSa). Da wannan bawan Allah Ya mutu ya koma ga Allah kuwa, sai Allah ﷻ Ya Yafe masa ɗin**[55]"

Allah ﷻ Ya saka masa ne da irin abinda ya kasance yake yiwa bayin Allah a rayuwarsa ta duniya. Da ma masu iya Magana suka ce Alkhairi danƙo ne, ba ya faɗuwa ƙasa banza.

Toh da yake ya kasance yana rangwanta wa bayin Allah mabuƙata a nan duniya saboda irin tsananin tausaya musu da yakeyi, sai shi ma Allah ﷻ Ya saka masa da irin wannan sakamako a daidai lokacinda yake matuƙar buƙatan hakan. Har ma Allah ﷻ Yace masa: **"Mu muka fi cancanta mu rangwanta wa mabuƙata. Saboda haka kai ma jeka na yafe maka".**

## I. Musafaha a yayin da aka gamu ana gaisawa:

Musafaha a yayinda aka gamu ana gaisawa (bayan anyiwa juna Sallama), wannan ƙarin tabbaci ne gameda amincin da yake tsakanin 'yan-uwa Musulmi.

Riƙe hannun juna a yayin sallama, yana tafiyar da ƙiyayya da gaba tsakanin Musulmi, kuma yana cikin manyan alamun soyayya da ƙaunar juna da kuma 'yan-uwantaka.

[55] Bukhari (3480), Muslim (1562). Dukkansu daga Sahabi Abu-Hurairah ﷺ

Shi yasa babban Malami Al-Imamu Hasanul-Basriy (Allah Ya Gafarta masa) Yake cewa: “Musafaha tana ƙara ƙauna (tsakanin musulmi). Idan ɗayanku yayi musafaha da ɗan-uwansa, toh ya riƙe hannunsa da kyau, domin hakan yana ƙara danƙon ƙauna (tsakaninsu). Kuma ko da yana ɗan jin wani ƙaiƙayi a zuciyarsa gameda shi, toh hakan zai warware wannan ƙulli (wanda shaiɗan ya tufka masa a zuciya gameda ɗan-uwansa musulmi)[56]”.

Sannan kuma Musafaha tana tsaftace bawa daga dattin zunubai, domin kuwa hadisai masu yawa sun tabbatar da cewa lallai ita ma musafaha tana daga cikin hayoyin samun Gafarar Allah ﷻ.

Manzon Allah ﷺ yana cewa: “**Babu wasu Musulmai biyu da za su gamu kuma suyi musafaha (a yayin sallama, gaisuwa irin ta Addinin Musulunci) fahce sai an Gafarta musu (zunubansu) kafin su rabu**[57] **(kafin su saki hannun junansu)**”.
Da fatan Allah Yasa mu dace.

Manzon Allah ﷺ yace: “**Lallai shi mumini idan ya gamu da (wani ɗan-uwansa) mumini, sai yayi masa sallama, sannan ya riƙe hannunsa suka gaisa; toh zunubansu za su riƙa kakkaɓowa (daga jikinsu) kamar yadda (busassun) ganyayyakin bishiya suke zubowa ƙasa idan iska ta kaɗa su**[58]”

Yana da kyau a kiyaye, kuma a riƙa raya wannan Sunnah, saboda fatan samun wannan falala mai yawan gaske da aka ambata cikin wannan ingantaccen hadithi mai daraja.

---

[56] Duba: Amaaliy na Ibnu Sam’un Al-waa’iz, majalisi na 14, juz’i na farko, sahafi na 230
[57] Abu-Dawud (hadithi na 5212) daga Sahabi Baraa’u ɗan Aazib Allah Ya ƙara musu Yarda
[58] Imam Aɗ-ɗabaraniy ne ya ruwaito shi a cikin littafinsa mai suna “Mu’jamul-Ausaɗ” (Juz’i na farko, shafi na 84, kuma hadisi na 245) daga Sahabi Huzaifah ɗan Yamaniy ؓ

Ba daidai ba ne irin durƙuson nan da akeyi ko rusunawa da sunan wai girmamawa, da dai sauran nau'ukan gaishe-gaishe waɗanda suka samo asali daga al'adun al'ummomi daban daban. Wannan kwata-kwata ba gaisuwar Musulunci ba ce. Karantarwar Manzon Allah ﷺ ita ce **riƙe hannun juna ayi musafaha**. Bayan ɗumbin falalar da yake tattare da su, mun ji kuma cewa hakan yana cikin hanyoyin samun Gafarar Allah ﷻ.

Sannan kuma ba ya halatta Musulmi yayi musafaha da wata mace wacce ba muharramarsa ba. Haka kuma irin wannan musafaha da wasu suke yi suna wasa da 'yan yatsu (har ma a wasu lokutan ana motsa wa juna sha'awa), wannan ba karantarwar musulunci ba ce. Amma in har matarka ce ka kama hannunta, wannan babu matsala, domin kuwa ita kam ta halatta gareka da ma.

Haka nan kuma ba sunnah ba ne yin musafaha da hannu biyu dukka. Abinda ya tabbata a sunnah shi ne yi da hannu ɗaya kawai (kuma hannun dama, ga wanda yake da hannun dama ɗin kenan).

Malamai ma suna tsawatarwa gameda yadda wasu suka tsiri al'adar yin musafaha a daidai lokacinda aka sallame sallah. Har ma wasu sun ɗauka ko hakan ma mantacciyar sunnah ce suke rayawa. Ko shakka babu wannan bai da asali a cikin karantarwar Manzo ﷺ. Abinda ya tabbata a Sunnah dai, shi ne akwai wasu zikirorinda ake karantawa bayan an sallame sallah. Toh wannan shi ya kamata a shagaltu da shi, ba wai wata ƙirƙirarriyar musafaha ba.. Sai dai wannan ba zai hana daga baya a miƙawa juna hannu a gaiggaisa ba. Amma riƙe hakan a matsayin wata al'ada, toh wannan ne bai da asali a cikin karantarwar Manzon Allah ﷺ. Allah Yasa mu dace.

**J. Taruwa don karatun addini, da kuma darasin sa:**
Irin wannan taro yana daga cikin wasu manyan taruka guda uku waɗanda a cikinsu ne kaɗai ake samun Alkhairan duniya da lahira, koma bayan wasu tarukan da ba su ba. Domin kuwa acikin Suratun-Nisa'i (ayah ta 114) Allah ﷻ Yana cewa:

﴿لَّا خَيْرَ فِي كَثِيرٍ مِّن نَّجْوَاهُمْ إِلَّا مَنْ أَمَرَ بِصَدَقَةٍ أَوْ مَعْرُوفٍ أَوْ إِصْلَاحٍ بَيْنَ النَّاسِ ۚ وَمَن يَفْعَلْ ذَٰلِكَ ابْتِغَاءَ مَرْضَاتِ اللَّهِ فَسَوْفَ نُؤْتِيهِ أَجْرًا عَظِيمًا﴾ [النساء:١١٤]

"*Babu Alheri cikin da dama daga cikin tarukansu (su mutane), sai wanda a cikinsa akayi umurni da wata sadaka (da duk abinda zai amfanar da gangan jikin ɗan Adam), ko kuma (umurni da) wani kyakkyawan aiki (da duk abinda zai amfanar da ruhin ɗan Adam), ko kuma (tattaunawar da ta ƙunshi) sasantawa tsakanin mutane (don a samu wanzuwar zaman lafiya a cikin al'ummah). Toh duk wanda ya aikata (ɗaya daga cikin) wannan alhalin yana mai neman Yardar Allah ﷻ, nan gaba (a lahira) Za Mu bashi Lada mai Girma*"

Manzon allah ﷺ yana cewa: "**Babu wasu mutanen da za su taru a cikin ɗaya daga cikin ɗakunan Allah su riƙa karanta Littafin Allah kuma suna darasin sa a tsakankaninsu; fahce sai nitsuwa ta sauka akansu, kuma sai Rahama ta lulluɓe su, sannan kuma Mala'iku (na Rahma) za su kewaye su (da Umurnin allah ﷻ za su katange su daga dukkanin sharri), sannan kuma allah ﷻ zai ambace su a cikin waɗanda suke tare da shi**[59]".
Allah ﷻ zai ambaci sunayensu ɗaya bayan ɗaya a gaban Mala'ikunsa, sannan Yace musu (su Mala'ikun): "**Ina**

---

[59] Sahih Muslim (hadithi na 2689), daga Sahabi Abu-Hurairah ﷺ

**mai kafa ku shaida akan cewa lallai haƙiƙa na Gafarta musu[60] (baki ɗayansu)**"

Shi yasa akeso a kowanne lokaci mu riƙa ƙoƙarin halartan wuraren da ake karatun addini, da wurarenda ake wa'azi. Saboda akwai falala mai ɗumbin yawa a waɗannan wurare.
Daga cikinsu dai, akwai samun Gafarar Allah ﷻ.

**Shi yasa aka shar'anta mana karanta "Kaffaratul-Majlis"..**
A duk lokacinda aka zo tashi daga inda ake zaune[61] toh a riƙa karanta wannan addu'a wacce ake kira **kaffaratul-majlis** (wato addu'ar neman gafarar Allah ﷻ gameda zunuban da aka aikata a cikin wannan zama da akayi).

Ga yadda addu'ar take:

سُبْحَانَكَ اللَّهُمَّ وَبِحَمْدِكَ، أَشْهَدُ أَنْ لَا إِلَهَ إِلَّا أَنْتَ، أَسْتَغْفِرُكَ وَأَتُوبُ إِلَيْكَ

Ma'ana: "**Dukkan Tsarki da Yabo da Godiya sun tabbata gareKa Ya Allah. Na shaida lallai babu abin bauta (bauta ta gaskiya a bisa cancanta) sai Kai (Kai kaɗai kake, baka da abokin tarayya). Ina neman GafararKa kuma na tuba zuwa Gareka**[62]"

Manzon Allah ﷺ ya kasance yana karanta wannan addu'a a duk lokacinda yazo tashi daga inda yake zaune. Kuma yace duk wanda yake yin haka, toh Allah ﷻ Zai yafe masa zunuban sa.

**K. Zikiri (ambaton Allah ﷻ)**

---

[60] Bukhari (2408), Muslim (2689), daga Sahabi Abu-Huraira رضي الله عنه
[61] Ko a ina ne (sawa'un wurin karatu ne ko wata ganawa, ko hira, ko wani aiki, ko kasuwanci da dai sauransu)
[62] Tirmidhi (hadithi na 3433), Ahmad (hadithi na 10420), daga Sahabi Abu-Huraira رضي الله عنه

Acikin Suratul-Ahzab (Ayah ta **35**) Allah ﷻ Ya lissafa masu yawan zikiri cikin waɗanda Yayi musu tanadin Gafara da kuma lada mai yawa. Yace:

﴿وَٱلذَّٰكِرِينَ ٱللَّهَ كَثِيرًا وَٱلذَّٰكِرَٰتِ أَعَدَّ ٱللَّهُ لَهُم مَّغۡفِرَةً وَأَجۡرًا عَظِيمًا ٣٥﴾

"*Har da kuma maza da mata masu zikiri da yawa, toh (baki ɗayansu) Allah Ya musu tanadin Gafara da kuma wata Lada mai Girma*".

Akwai hadisai masu yawa da suke tabbatar da cewa lallai bawa zai samu Gafarar Allah ﷻ matuƙar yana yawan ambatonSa kamar yadda Shari'a ta karantar. Daga cikin zikirorin da Manzon Allah ﷺ ya kwaɗaitar damu mu riƙa karanta su don samun Gafara da kuma lada mai yawa, akwai waɗannan:

## Zikirorin safe da yamma:

a. Karanta wannan addu'a wacce ake kira **Sayyidul-Istighfar** **(**mafi girma cikin addu'o'in neman Gafara**)** safe da yamma:

**اللَّهُمَّ أَنْتَ رَبِّي لاَ إِلَهَ إِلَّا أَنْتَ، خَلَقْتَنِي وَأَنَا عَبْدُكَ، وَأَنَا عَلَى عَهْدِكَ وَوَعْدِكَ مَا اسْتَطَعْتُ، أَعُوذُ بِكَ مِنْ شَرِّ مَا صَنَعْتُ، أَبُوءُ لَكَ بِنِعْمَتِكَ عَلَيَّ، وَأَبُوءُ لَكَ بِذَنْبِي فَاغْفِرْ لِي، فَإِنَّهُ لاَ يَغْفِرُ الذُّنُوبَ إِلَّا أَنْتَ**

"*Ya Allah Kai ne Ubangiji na, babu abin bauta (bauta ta gaskiya a bisa cancanta) sai Kai. Kai ne Ka halicce ni. Kuma ina nan kan umurnin nan naKa (da Kayi wa bayinKa) da kuma alƙawarin nan naka (wanda yake tsakaninKa da bayinKa) gwargwadon iyawa ta. Ina neman tsarin Ka daga sharrin abinda na aikata (na laifi). Ina mai iƙirari (da kuma godiya gareKa) gameda ni'imominKa a kaina (waɗanda babu wanda yasan yawansu sai Kai). Na na tabbatar lallai ina da zunubai (masu yawa), ina kuma neman Ka Gafarta min, domin kuwa babu mai Gafarar zunubai sai Kai*".

Manzon Allah ﷺ yace: "**Lallai duk wanda ya faɗe ta da rana alhali yana mai yaƙini da ita**[63]**, sannan sai yam utu a ranar kafin maraice, toh yana cikin 'yan Aljannah. Haka kuma duk wanda ya faɗe ta da dare alhalin yana mai yaƙini da ita, sai yam utu kafin asubahi, toh yana cikin 'yan Aljannah**[64]"

Ko shakka babu wannan addu'a tana da muhimmanci sosai. Ya kamata mu haddace ta, musan ma'anarta, mu koya wa iyalanmu, kuma mu riƙa karanta ta a kullum. Da fatan Allah Yasa mu dace.

**b.** Kuma a riƙa karanta wannan zikirin sau ɗari (**100**) a rana:

لَا إِلَهَ إِلَّا اللَّهُ، وَحْدَهُ لَا شَرِيكَ لَهُ، لَهُ الْمُلْكُ، وَلَهُ الْحَمْدُ، وَهُوَ عَلَى كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ

"**Babu abin bauta da gaskiya a bias cancanta sai Allah, Shi kaɗai Yake Bai da abokin tarayya, dukkan Mulki da dukkan yabo da godiya naShi ne (Shi kaɗai), kuma Shi ne Mai cikakken iko akan dukkan komai**"

Manzon Allah ﷺ yace duk wanda ya karanta ta sau ɗari a rana, "**toh daidai yake da wanda ya 'yanta bayi goma**[65]**, za kuma a rubuta mishi kyawawan ayuka har guda ɗari**[66]**, a kuma kankare masa munanan ayuka guda ɗari. Sannan kuma (wannan addu'a) za ta zame masa (wata irin) kariya daga shaiɗan a duk wannan yini har zuwa maraice. Haka nan kuma babu wanda zai zo (a lahira) da aikinda yafi (wannan aikin) nashi falala sai wanda ya aikata sama da abinda ya aikata**[67]"

[63] Wato ya ƙudurce a zuci cewa da gaske neman gafara yake, kuma ya yarda cewa Allah Shi ne kaɗai Mai Gafarta wa bayi

[64] Sahihul-Bukhari (hadithi na **6306**) daga Sahabi Shaddau ɗan Aus ﷺ

[65] Mun riga kuma mun ga irin falalar da 'yanta bawa ɗaya ma yake da ita a can baya.

[66] Tare da kuma duk wani kyakkyawan aiki guda ɗaya ana ninka shi sau goma ne har zuwa sau 700 ko ma fiye da hakan, gwargwadon baiwar da Allah ﷻ Yayiwa bawanSa.

[67] Sahihul-bukhari (**3293**), Sahih-muslim (2691), daga Sahabi Abu-Huraira ﷺ

Wannan zikiri yana da matuƙar muhimmanci sosai. Saboda yana jaddada tauhidin bawa, kuma Yana ƙara masa ƙarfin imani da kuma yaƙini da tawakkali, sannan kuma yana cire wa bawa tsoron wata halitta.

Daga cikin Hanyoyin Samun Gafarar Allah, akwai faɗin waɗannan kalamai masu daraja sau ɗari a rana, wato a ce:

سُبْحَانَ اللَّهِ وَبِحَمْدِهِ

"**Dukkan Tsarki da Godiya sun tabbata ga Allah**"

Manzon Allah ﷺ yace duk wand ya faɗi wannan zikiri sau ɗari (100) a rana guda, "**Za a Gafarta masa zunubansa ko da kuwa sun kai kwatankwacin (yawan) kumfar teku ne**[68]" Waɗannan kalmomi dai suna da sauƙin faɗi, ga daɗi da kuma zaƙin furtawa. Allah ﷻ ne Ya zaɓa mana su don mu riƙa furtawa don mu samu GafararSa. Mu riƙa kula da kyau, kar mu manta da wannan Sunnah, saboda mu ma mu samu Rahamar Allah ﷻ.

Sai dai abin takaici yanzu za ka iske mutum musulmi yana da lokacin zama yayi ta zabga surutu a wajen hira, yana da lokacin sauraren duk wata waƙa da duk wata sharholiya, amma bai da lokacin da zai iya warewa domin nitsuwa ya ambaci Allah ﷻ. Allah Ya tsare mu daga sharrin shaiɗan.

**A yayin da aka ji kiran sallah**

Idan aka ji Ladani yana Kiran Sallah, toh ana so kowa ya maida hankali ya saurara da kyau. Saboda a daidai wannan lokaci akwai wasu zikirorin da Manzon Allah ya umurce mu da mu riƙa furtawa.

---

[68] Sahihul-Bukhari (Hadithi na 6405) daga Sahabi Abu-Huraira ؓ

Daga cikinsu akwai:

**أَشْهَدُ أَنْ لَا إِلَهَ إِلَّا اللهُ وَحْدَهُ لَا شَرِيكَ لَهُ، وَأَنَّ مُحَمَّدًا عَبْدُهُ وَرَسُولُهُ، رَضِيتُ بِاللهِ رَبًّا وَبِمُحَمَّدٍ رَسُولًا**

**"Na shaida babu abin bauta (a bisa cancanta) sai Allah ﷻ, Shi kaɗai Yake Bai da abokin tarayya. Kuma lallai Annabi Muhammadu bawanSa ne kuma ManzonSa. Na yarda da Allah a matsayin Ubangiji. Na yarda da muhammadu a matsayin Manzo. Na kuma yarda da Musulunci a matsayin Addini (wanda dole sai ta hanyarsa kaɗai za a bauta wa Allah ﷻ Ya karɓa)"**

Manzon Allah ﷺ yace duk wanda ya faɗi wannan zikiri (a irin wannan lokacin) "**za a Gafarta masa zunubansa**[69]"

## Faɗin Kalmar "Ameen" a Yayinda aka kai Karshen Suratul-Fathiha

Manzon Allah ﷺ yana cewa: "**Yayinda Liman ke faɗin Ameen, toh ku ma ku faɗa (tare da shi). Domin kuwa duk wanda faɗinsa ya dace da faɗin Mala'iku, toh za a Gafarta masa abinda ya gabata na zunuban sa**[70]".

## Zikirin da ake Karantawa Yayin Ɗagowa daga Ruku'u

Idan aka ɗago daga ruku'u, Limami yana cewa:

**سَمِعَ اللَّهُ لِمَنْ حَمِدَهُ**

**"Allah Yana jin mai gode Masa (Kuma Yana amsa addu'ar duk mai roƙon Sa)"**

Shi kuma mamu sai yace:

**اللَّهُمَّ رَبَّنَا وَلَكَ الْحَمْدُ**

**"Ya Allah Ubangijina, dukkan yabo da godiya sun tabbata gareKa (Kai kaɗai baKa da abokin tarayya)"**.

[69] Sahih-Muslim (Hadithi na 387) daga Sahabi Sa'adu ɗan Abu-waƙƙas ؓ
[70] Sahihil-Bukhari (Hadisi na **780** ) daga Sahabi Abu-Huraira ؓ

Haka Manzon Allah ﷺ yayi umurni. Kuma yace duk wanda ya faɗi hakan sannan ya dace da na Mala'iku, **to shi ma za a Gafarta masa abinda ya gabata na zunubansa**[71]".

## Zikirin da ake karantawa bayan Sallama:

Idan aka sallame sallah ma, ai akwai wasu addu'o'I da zikrori daban-daban waɗanda Sunnah ta koyar a riƙa karantawa kafin a tashi[72].

Daga cikinsu akwai Tasbihi sau 33, Hamdala sau 33, kabbara sau 33, daga ƙarshe kuma a cike da faɗin:

**لَاإِلَهَ إِلَّا اللهُ وَحْدَهُ لَاشَرِيكَ لَهُ، لَهُ الْمُلْكُ وَلَهُ الْحَمْدُ، وَهُوَ عَلَى كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ**

"**Babu abin bauta da gaskiya a bisa cancanta sai Allah ﷻ, Shi kaɗai Yake bai da abokin tarayya, dukkan mulki da godiya baki ɗaya naShi ne (Shi ne Mamallakin komi da kowa, kuma Shi ne cikakken abin yabo gameda komai), Kuma shi mai cikakken iko ne akan dukkan komai**".

Duk wanda ya karanta waɗannan zikirorin kamar yadda aka ambata, Manzon Allah ﷺ yace **"Za a Yafe masa laifukansa ko da kuwa sun kai kwatankwacin yawan kumfar teku ne**[73]**"**

## A yayin da aka gama cin abinci (ko abin sha).

Yin **Hamdalah** bayan an gama cin abinci, yana daga cikin muhimman hanyoyin samun gafara, musamman ma karanta wannan addu'a kamar haka:

---

[71] Bukhari (Hadisi na 796) daga Sahabi Abu-Huraira ؓ

[72] Zikrorin nan fa dole ne sai irin waɗanda Manzon Allah ﷺ ya karantar kawai za ayi (babu ƙari babu ragi).

[73] Sahih-Muslim (Hadithi na 597) daga Sahabi Abu-Huraira ؓ

**الْحَمْدُ لِلَّهِ الَّذِي أَطْعَمَنِي هَذَا الطَّعَامَ وَرَزَقَنِيهِ مِن غَيْرِ حَوْلٍ مِنِّي وَلاَ قُوَّةَ**

"**Dukkan yabo da godiya sun tabbata ga Allah wanda Ya ciyar da ni wannan abincin, kuma Ya arzuka ni da shi ba tare da wata dabara ta ko ƙarfi daga gareni ba**".

Manzon Allah ﷺ yace "**duk wanda ya karanta wannan addu'a bayan ya agama cin abinci, toh za a Gafarta masa abinda ya gbata na zunubansa**"

## L. Jihadi don ɗaukaka addinin Allah:

Jihadi shi ne tozon Addinin Musulunci[74]. Kuma Kasuwanci ne mai riba sosai tsakanin bawa da Mahaliccinsa. A cikin Suratut-Taubah (ayah ta 111) Allah ﷻ Yace:

﴿إِنَّ ٱللَّهَ ٱشْتَرَىٰ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ أَنفُسَهُمْ وَأَمْوَٰلَهُم بِأَنَّ لَهُمُ ٱلْجَنَّةَ ۚ يُقَٰتِلُونَ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ فَيَقْتُلُونَ وَيُقْتَلُونَ ۖ وَعْدًا عَلَيْهِ حَقًّا فِى ٱلتَّوْرَىٰةِ وَٱلْإِنجِيلِ وَٱلْقُرْءَانِ ۚ وَمَنْ أَوْفَىٰ بِعَهْدِهِۦ مِنَ ٱللَّهِ ۚ فَٱسْتَبْشِرُوا۟ بِبَيْعِكُمُ ٱلَّذِى بَايَعْتُم بِهِۦ ۚ وَذَٰلِكَ هُوَ ٱلْفَوْزُ ٱلْعَظِيمُ﴾

"*Lallai Allah ﷻ Ya sayi rayukan Muminai da kuma dukiyoyinsu, cewa lallai suna da Aljannah (a matsayin abinda za a biya su da shi). Suna yin (amfani da dukiyoyin nasu da kuma rayukansu wajen) yaƙi cikin (ɗaukaka) tafarkin Allah, domin kuwa (a fagen daga ) suna kashewa kuma su ma ana kashesu. Alƙawari ne tabbatacce wanda Allah ﷻ Yayi acikn (littatafan) At-Taurah da Injila da kuma Al-Kur'ani, kuma babu cikakken mai cika alƙawarinda ya ɗauka irin Allah ﷻ. Saboda haka ku kasance cikin Albishir saboda wannan cinikin naku da kuka ƙulla daShi. Kuma wannan shi ne babban rabo mai girman gaske.*"

[74] Sahih Muslim (Hadithi na 121) daga Sahabi Amru ɗan Aas ؓ

Jihadi don ɗaukaka Addinin Allah ﷻ, wani irin kasuwanci ne wanda baki ɗayansa riba ce zallah babu faɗuwa, domin kuwa da Allah ﷻ aka ƙulla shi. Saboda haka ma daga cikin farashinsa akwai Gafarar Allah da kuma Aljannah (bayan nasarar da Allah Yayi alƙawarin Zai baiwa duk wanda ya tsaya ya kyautata niyyah yayi Jihadin da gaske).

A cikin Suratus-Saff (ayah ta **10** zuwa ta **13**) Allah ﷻ Yana cewa:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ هَلۡ أَدُلُّكُمۡ عَلَىٰ تِجَٰرَةٖ تُنجِيكُم مِّنۡ عَذَابٍ أَلِيمٖ ١٠ تُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَتُجَٰهِدُونَ فِي
سَبِيلِ ٱللَّهِ بِأَمۡوَٰلِكُمۡ وَأَنفُسِكُمۡۚ ذَٰلِكُمۡ خَيۡرٞ لَّكُمۡ إِن كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ١١ يَغۡفِرۡ لَكُمۡ ذُنُوبَكُمۡ وَيُدۡخِلۡكُمۡ جَنَّٰتٖ
تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ وَمَسَٰكِنَ طَيِّبَةٗ فِي جَنَّٰتِ عَدۡنٖۚ ذَٰلِكَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ١٢ وَأُخۡرَىٰ تُحِبُّونَهَاۖ نَصۡرٞ مِّنَ ٱللَّهِ
وَفَتۡحٞ قَرِيبٞۗ وَبَشِّرِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ١٣ ﴾

"*Ya ku waɗanda kukayi imani! Shin (kuna so) in nuna muku wani irin kasuwanci wanda zai zama sanadiyyar tsirar ku daga azaba mai raɗaɗi?"*
*Wannan kasuwanci shi ne; Kuyi imani da Allah* ﷻ *da ManzonSa r, kuma kuyi Jihadi don ɗaukaka tafarkin Allah. Wannan dai shi ne (yafi zama) Alhairi gareku in har da kun kasance kun sani".*
*Zai Gafarta muku zunubanku kuma Zai shigar daku Aljannatai waɗanda koramu (na ababen sha iri-iri) suke gudana a ƙarƙashinsu, Zai baku wasu irin kyawawan gidaje masu daɗin zama a cikin waɗannan aljannatai waɗanda suke an riga ayi tanadinsu, wannan dai babban rabo ne. Kuma akwai ma sauran (wasu nau'uka na tukuici) na daban waɗanda (tabbas) kuna son su (a wannan rayuwa ta duniya),*

*su ne; Taimako daga Allah*[75] *da cin nasara (akan abokan gab) wanda yake nan kusa (za ku samu in har kuka ƙara ƙanƙame wannan tafarki madaidaici). Kuma (Ya Muhammadu) kayiwa Muminan nan (masu Jihadi) bishara (domin kuwa duk abinda suke buƙata a duniya da lahira sakamakon wannan jajircewa da sukayi don kare wannan Addini)*".

Allah ﷻ Ya yi alƙawarin Gafarta wa Mujahidai; domin kuwa dasu Yake yaɗa addininSa, dasu Yake kare addinin, kuma dasu Yake ɗaukaka shi akan duk wani addini na daban wanda ba shi ba. Matuƙar musulmi sunyi riƙo da karantarwar wannan Addini na Allah ﷻ, toh kuwa ba za su taɓe ba har abada.
A cikin Suratul-Anfal (ayah ta 74) Allah ﷻ Yana cewa:

﴿ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَهَاجَرُوا۟ وَجَٰهَدُوا۟ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱلَّذِينَ ءَاوَوا۟ وَّنَصَرُوٓا۟ أُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُؤْمِنُونَ حَقًّا ۚ لَّهُم مَّغْفِرَةٌ وَرِزْقٌ كَرِيمٌ ﴾

"*Su kuma waɗanda sukayi imani kuma sukayi kuma sukayi Jihadi don ɗaukaka Tafarkin Allah, da (sauran Muminai) waɗanda suka bayar da masauki (ga masu hijira) kuma sukayi taimako (da duk abinda Allah ﷻ Ya hore musu don ɗaukaka Addinin Allah); waɗannan (baki ɗayansu) su ne muminai na gaskiya. Suna da Gafara da kuma wani irin arziki mai yawa (na ababen ci da sha da duk sauran ababen more rayuwa) irin na girmamawa*".

---

[75] Ta hanyar ƙara tabbatar da ku akan wannan tafarki madaidaici,Ya kuma karya lagwan abokan gaba har kuyi galaba akansu.

Allah ﷻ Ya musu tanadin wasu irin gidaje na alfarma acikin Aljannah.
Manzon Allah ﷺ Yana cewa: "**Lallai a cikin Aljannah akwai wasu irin (benaye masu) darajoji ɗari (hawa 100) waɗanda Allah ﷻ Yayi tanadin su ga masu Jihadi saboda ɗaukaka AddininSa. Tsakanin kowacce daraja da wacce take sama da ita kamar nisan da yake tsakanin sama da ƙasa**[76]".

## M. Mutuwar Shahada[77]

Mutuwar Shahada (Shahada ta gaskiya) tana daga cikin manyan ni'imomin da Allah Yake yi ga wasu zaɓaɓɓu daga cikin bayinSa na ƙwarai. Kuma duk wani Salihin bawa ya kasance yana fatan samun wannan daraja ta shahada.

Saboda; bayan ɗumbin lada da kuma falalar da take da su masu yawa, tana ma cikin manya-manyan hanyoyin samun Gafarar Allah ﷻ.
Bayan ayoyin Al-Kur'ani, akwai Hadisai ma masu yawa da sukayi bayanin falalar mutuwar Shahada.

## Falalar mutuwar Shahada

Ga kaɗan daga cikinsu[78] insha'Allah:
**a.** Za a yafe wa mai mutuwar Shahada laifukansa tun daga ɗigon jininsa na farko a lokacinda yazo mutuwa.
**b.** Tun a lokacin za a nuna masa mazauninsa na cikin Aljannah.

---

[76] Sahihul-Bukhari (hadithi na 2790) daga Sahabi Abu-Huraira ؓ
[77] Mutuwar mumini a yayinda yake fafitikar kare Addini a fagen daga, ko kuma a kashe shi a yayinda yake faman kare mutuncinsa ko mutuncin iyalansa, ko kuma a yayinda yake faman kare dukiyarsa, ko kuma wata hanya daga cikin hanyoyin da shari'ah tayi bayani. Allah Ya arzukta mu da irin wannan mutuwa.
[78] Daga kan "**a**" zuwa "**g**" duk sun zo a dunƙule cikin hadisi guda, duba: Tirmizi (**1663**) daga Miƙdaamu Ibn Ma'adiy-karib ؓ

c. Za a amintar dashi daga fitinar Kabari (ba za a fitine shi ba, kuma ba za a azabtar da shi ba).
d. Za a amintar da shi daga wannan firgici mafi girma na ranar ƙiyamah (saboda haka bai da fargaba kuma babu baƙin ciki tare da shi har abada[79]).
e. A lahira za a ɗaura masa wani irin kambe na girmamawa a kansa, na yaƙutu, wanda guda ɗaya daga cikinsu ya fi duk duniya da abinda yake cikinta.
f. Za a ɗaura masa aure da wasu mata na musamman (har su **72**) daga cikin matan Aljannah (tun a lokacinda ake zare ran shi daga gangar jikinsa).
g. Kuma a lahira za a bashi damar ceton har mutum 70 daga cikin danginsa.
***** Ba ya jin zafin fitar rai, sai kamar gwargwadon zafin cizon cinyaka[80]
*****A cikin Aljannah kuma, zai riƙa burin inama ayi ta dawo dashi duniya a ƙara kashe shi ta wannan hanya har sau goma. Ba don komi ba sai saboda irin abinda ya gani na falalar shahada[81], da irin girmamawar da ya samu a cikin Aljannah.

Waɗannan dai suna daga cikin jerin falalolin da mutuwar shahada ta gaskiya take tattare da su. Na ce **shahada ta gaskiya** ne, saboda akwai waɗanda ba na gaskiya ba. Toh su (na ƙaryan) banda su a cikin waɗanda za su samu wannan falalar da akayi bayani. Domin kuwa babu wanda zai samu sai wanda ya cika sharuɗan karɓar ibada (wato yi don neman Yardar Allah ﷻ, da kuma dacewa da karantarwar Manzon Allah ﷺ).

[79] Za atsare masa iyalansa (waɗanda ya mutu ya bari a duniya), ba za su tagayyara ba, kuma insha'Allah ba za su kauce hanya ba su ma.
[80] Imam Ahmad (**7953**), Tirmizi (1668), Nasa'i (**3161**), Ibn Hibban (**4655**).. Daga Abu-Huraira ﷺ.
[81] Bukhari (**2817**), Muslim (**1877**) duk daga Sahabi Anas ɗan Maalik ﷺ

Za mu gane hakan ne idan muka san kashe-kashen shahada. Ga su nan (a gurguje) kamar haka insha'Allah.

## Nau'ukan shahada:

Saboda lura da nassoshin Al-Kur'ani da kuma ingantattun hadithai, Malamai sun karkasa nau'ukan shahada zuwa kashi uku. Su ne kamar haka:

1) Sukace akwai masu hukuncin shahda a duniya kaɗai, banda lahira.
Su ne waɗanda a idanun mutane dai mutuwar shahda sukayi, amma a wajen Allah su ba shahidai ba ne, saboda basu cika sharuɗan karɓar aiki ba.
Su ba shahidan gaskiya ba ne. Shahidan ƙarya ne. Amma da yake babu wanda yasan matsayinsu sai Allah ﷻ (Masanin baki ɗaya ɓoyayyu da bayyanannun al'amura), toh dole za ayi musu yadda ake wa shahidan gaskiya anan duniya.
Don haka ba za ayi musu wanka ba kuma ba za ayi musu Sallah ba, A hakan za a ɗaukesu cikin jinin nasu aje a binne a maƙabartar Musulmi (tunda a filin yaƙi aka kashesu, kuma babu wanda yasan abinda suka ƙudurce a zuci sai Allah ﷻ).
-Su ne irin munafukan nan waɗanda saboda ƙwarewa a munafunci har ma sun kai ga suna bin Musulmin ƙwarai Jihadi (saboda wasu manufofi nasu na karan kansu), sai kuma suyi rashin sa'a ta ritsa da su a cikin gumurzun yaƙi a kashe su a can.
-Daga cikin masu irin wannan hukunci akwai wanda zai tashi yaje filin jihadi kuma a kashe shi a chan, amma ba don kare addinin Allah yaje ba shi kam. Ya je ne kawai don ya nuna wa duniya cewa shi ma fa jarumi ne.

Waɗannan kam a lahira basu da komai awajen Allah sai azaba mai tsanani. Suna ma cikin jerin mutum uku waɗanda

dasu ne za a hura wutar jahannama a ranar (su zasu fara shiga wuta kafin duk wani kafiri).

2) Akwai kuma mai hukuncin shahada a lahira kaɗai banda duniya. Shi kam ana wanke gawarsa, kuma ana masa Sallah, sannan aje a binne shi a maƙbartan Musulmi.
Shi ne wanda ya mutu ta ɗaya daga cikin waɗannan hanyoyi (alhalin yana musulmi):
-Wanda ya mutu a yayin kare dukiyarsa, da mutuncinsa dana iyalansa,
-Wanda akayiwa kisar gilla saboda kaɗai ya yi riƙo da Addinin Allah, ko ma yana kira zuwa gareshi (amma ba a filin yaƙi aka kasheshi ba),.
-Irin wanda ruwa ya cinye shi,
-Wanda gini ya rushe akansa ya kashe shi,
-Wanda gobara ta zama ajalinsa,
-Wanda ya mutu sanadiyyar wata annoba ta cuta da ta ɓarke a garinda yake,
-wanda ya mutu sanadiyyar ciwon ciki (irin matsanacin ciwon cikin nan mai murɗe mutum ya kasha shi lokaci guda,
-Wacce ta mutu sakamakon wahalar naƙudar haihuwa,
Da dai sauran makamantansu waɗanda hadisai sukayi bayanin cewa su ma suna da darajar shahada.
Saboda haka za su samu falalar da shahidin gaskiya yake samu gwargwadon hali insha'Allah.

3) Sannan akwai kuma wanda aka fi sani da wannan suna na shahidi, wato mai hukuncin shahada a duniya da lahira baki ɗaya.
Shi ne Muminin da aka kashe shi a filin yaƙi tsakanin musulmi da kafirai.
Wannan a duniya hukuncin gawarsa daban ne da sauran gawaki. Domin kuwa ba a masa wanka, kuma ba a masa

Sallah. Haka za a ɗauke shi cikin jinin nashi a binne shi a wurinda ya mutu ɗin.
Sannan kuma a lahira, yana da waɗancan falalolin da aka ambata acikin ayoyi da ingantattun hadithan da sukayi bayanin falalar mutuwar shahada. Daga falalolin dai, akwai samun Gafarar Allah ﷻ.
Allah ﷻ Zai Yafewa duk wanda yayi mutuwar shahada da kyakkyawar niyyah (kuma yake kan tafarkin Manzon Allah ﷺ). Zai yafe masa baki ɗaya zunuban da ya aikata. Amma fa laifukanda yayiwa Allah ne kaɗai za a yafe masa, banda haƙƙin mutane[82].

Domin kuwa Manzon Allah ﷺ ya ce: "**Allah ﷻ Zai Gafarta wa Shahidi dukkan komai (na laifinda ya aikata a rayuwarsa) fahce bashi**[83] **(wanda wasu suke binsa)**".

Allah Yasa mu gama da duniya lafiya, Ya tsare mu daga taurin bashi da kuma rinjayen maƙiya, da kuma mummunan abin ji da mummunan abin gani a duniya da lahira.

Allah Ya Arzukta mu da mutuwar Shahada ta gaskiya.

***

**(Hanya ta Bakwai)**

**Haƙurin bawa a bisa wata jarrabawar da ta same shi**

**(sawa'un a jikinsa ne ko iyalansa ko dukiyarsa)**

---

[82] Idan akwai haƙƙin wani akansa kam, toh wannan hukuncinsa daban. Mun riga mun ga bayani akan wannan tun a farkon wannan littafi, inda aka lissafo sharuɗan tuba. Allah Yasa mu dace.

[83] Sahih-Muslim (hadithi na 1886) daga Sahabi Abdullah ɗan Amru ɗan Aas (shi da Mahaifin naashi baki ɗayansu sahabbai ne) Allah Ya ƙara Yarda dasu.

Jarrabawa sunnar Allah ﷻ ce. Rayuwar ma baki ɗayanta jarrabawa ce. Domin kuwa an kawo mu duniya ne don mu rayu a cikinta na wani lokaci, wanda a ciki ne za mu aikata abinda za a saka mana da shi bayan mutuwar mu.

Allah ﷻ Yana cewa (a farkon Suratul-Mulk):

﴿ بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ ۝ تَبَٰرَكَ ٱلَّذِي بِيَدِهِ ٱلۡمُلۡكُ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٌ ١ ٱلَّذِي خَلَقَ
ٱلۡمَوۡتَ وَٱلۡحَيَوٰةَ لِيَبۡلُوَكُمۡ أَيُّكُمۡ أَحۡسَنُ عَمَلٗاۚ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡغَفُورُ ٢ ﴾

"*Albarkatun (Allah) sun yawaita, wanda baki ɗaya mulki (mallakar komi da kowa) a hannunSa yake, kuma Shi ɗin mai cikakken iko ne akan dukkan komai. Shi ne wanda wanda Ya halicci mutuwa da rayuwa baki ɗaya, domin Ya jarraba ku (Ya ware su waye ne) daga cikinku masu kyautata ayukansu. Kuma Shi ne Mabuwayi Mai Gafara*".

Kowa daga cikin mutane akwai nau'in jarabawar da Allah ﷻ Yake masa a rayuwa. Akwai waɗanda ake jarabtar su da jin daɗin rayuwa, akwai kuma waɗanda ake jarabtar su da wahalhalun rayuwa.

Wasu ana jarabtar su ta dukiyoyinsu, wasu ta iyalansu, wasu ta mulkinsu, wasu ta lafiyarsu, wasu ta iliminsu (na addini ko na zamani), wasu ma ta sashen addininsu, da dai sauransu. Kowa ana jarabtar shi ta waɗannan fannoni na rayuwa (da ma sauran da ba'a ambata ba) imma da jin daɗi ko kuma akasin hakan.

Allah ﷻ Yana cewa:

﴿ كُلُّ نَفۡسٖ ذَآئِقَةُ ٱلۡمَوۡتِۗ وَنَبۡلُوكُم بِٱلشَّرِّ وَٱلۡخَيۡرِ فِتۡنَةٗۖ وَإِلَيۡنَا تُرۡجَعُونَ ﴾ [الأنبياء:٣٥]

"*Kowacce rai (dole) za ta ɗanɗani mutuwa. Kuma Muna jarabtar ku da sharri (dangin ababenda kuke ƙi) da kuma*

*Alkhairi (dangin ababenda kukeso) don kawai Mu gwada ku. Kuma gareMu za ku koma (Mu baku sakamakon duk abinda kuka aikata a rayuwarku ta duniya)*"

## Ga abinda ya dace bawa yayi idan Allah ﷻ Ya jarabce shi da wani abu na jin daɗin rayuwa:

Lallai kam daga cikin mutane akwai wanda za a bashi ɗaukaka ko dukiya ko lafiya da sauran ababen jin daɗi na rayuwar duniya (wani za a haɗa masa masu yawa, wani kuma kaɗan, wani ma guda ɗaya za a bashi gwargwadon hali), ba don komi ba sai don a jarraba godiyarsa.
Mai rabo a wajen Allah ﷻ shi ne zai gode maSa akan duk wata ni'imar da Ya bashi. Hakan kuma zai zama sanadiyyar samun ƙari daga Allah ﷻ, da kuma albarkar rayuwa, da tsira daga uƙubarSa a duniya da lahira.
Shi kuma mara rabo, toh zai butulce yaƙi gode masa. Hakan kuma zai zama sanadiyyar fushin Allah da uƙubarSa gareshi a duniya da lahira (in har bai tuba ya koma ga Allah ba). Don haka a cikin Suratu Ibrahim عليه السلام (ayah ta 7) Allah ﷻ Yake cewa:

﴿ وَإِذْ تَأَذَّنَ رَبُّكُمْ لَئِن شَكَرْتُمْ لَأَزِيدَنَّكُمْ ۖ وَلَئِن كَفَرْتُمْ إِنَّ عَذَابِي لَشَدِيدٌ 7 ﴾

"*Tuna lokacinda Ubangijinku Ya shelanta cewa "Lallai in har kunyi godiya (gameda ni'imomin da Nayi muku) toh Zan ƙara muku. In muka kuka butulce, toh fa (ku sani) lallai azabah Ta mai tsanani ce*"

Allah ﷻ Ya bamu misalai masu yawa akan wannan al'amari a cikin wasu ayoyi na al-Kur'ani Mai girma, gameda masu gode miShi da kuma masu butulci.
Ya faɗi halaye da kuma sakamakon kowanne daga cikinsu.
Duk hanyar da mutum ya zaɓa 9sawa'un shiriya ce ko ɓata), toh akwai sakamakon da aka tanadar wa masu bin ta.

Kai tsaye za mu gutsuro kaɗan daga cikin kowanne ɓangare don buga misali insha'Allah. Da fatan Allah Maɗaukaki Ya sanya mu cikin bayinSa shiryayyu masu gode maSa, Ya tsare mu daga kasancewa ɓatattu masu butulce maSa. Daga cikin Misalan masu godiya akwai labarin Annabi Sulaimanu[84] ﷤. yayinda ya ga an bi umurninsa anyi abinda duk duniya babu sarkin wani gari da zai iya samun hakan); sai yace:

﴿هَٰذَا مِن فَضۡلِ رَبِّي لِيَبۡلُوَنِيٓ ءَأَشۡكُرُ أَمۡ أَكۡفُرُۖ وَمَن شَكَرَ فَإِنَّمَا يَشۡكُرُ لِنَفۡسِهِۦۖ وَمَن كَفَرَ فَإِنَّ رَبِّي غَنِيّٞ كَرِيمٞ﴾ [النمل:٤٠]

"*Wannan (lallai) falal ce daga cikin falalar Ubangiji na (ba iyawa ta bace ko dabara ta ko ƙarfin mulki na). Ya yi hakan ne kuma don Ya jarabce ni (Ya gani) shin godiya zanyi ko kuma zan butulce ne? Lallai duk wanda yayi godiya (ga Allah a bias wata ni'imar da Yayi masa) toh fa ya yi godiyar ne don kansa (saboda shi ne zai samu sakamakon aikinsa a gobe ƙiyamah). Wanda kuma ya butulce (ya ƙi godewa Allah, toh fa kansa yayiwa) domin kuwa lallai Ubangiji na cikakken Mawadaci ne kuma Mai Karimci*"

A farko-farkon Suratul-Isra'i Allah ﷻ Ya yabi bawanSa Annabi Nuhu ﷤ saboda shi bawa ne mai yawan godiya ga Allah, inda Yake cewa:

﴿إِنَّهُۥ كَانَ عَبۡدٗا شَكُورٗا ٣﴾ [الإسراء:٣]

"*Lallai shi (Annabi Nuhu ﷤) ya kasance bawa ne mai yawan godiya*"

---

[84] Wanda shi Annabin Allah ne, kuma Allah ﷻ Ya baashi ilimi mai faɗin gaske, sannnan kuma Ya bashi mulki sama da na kowa daga cikin bayi, domin kuwa bayan mutane har ma da aljanu da dabbobi dukka yake mulka, kuma idan yayi umurni babu mai saɓa masa daga cikinsu.

Duk mai godiya ga Allah (godiya irin ta shari'a[85]) toh haƙiƙa yay i koyi da Annabawan Allah (Tsira da Amincin Allah su ƙara tabbata garesu baki ɗayansu).
Hakan zai sa Allah ﷻ Ya ƙara masa, kuma Ya albarkaci rayuwarsa, kuma Ya yarda da shi, kuma Allah ﷻ Zai tsare shi daga uƙubarSa ta duniya da lahira (irin wacce Yake yi wa masu butulci).
Wannan kenan!

Sannan akwai kuma irinsu ƙaruna, waɗanda suka butulce a yayinda suka ga sun bunƙasa. Sai Allah ﷻ Ya saukar da uƙubarSa akansu, Ya kawar da su.
Wasu Malamai daga cikin mutanensa sun yi ta masa wa'azi akan ya daina alfahari da kuma girman kai, saboda hakan ba ɗabi'a ce ta masu rabo a wajen Allah ﷻ ba. Shi kuma ƙaruna sai ƙara cika baki yakeyi yana ta taƙama. Bai ma yarda cewa wannan dukiyar tashi daga Allah take ba. Gani yake kamar iyawarsa ce ta bashi (saboda haka babu wanda zai godewa, kuma ba zai bi umurnin kowa ba).
Har ma yana hura hanci yana cewa cewa:

﴿إِنَّمَآ أُوتِيتُهُۥ عَلَىٰ عِلۡمٍ عِندِيٓۚ﴾ [القصص:٧٨]

"Ni fa (wannan dukiyar da kuke gani) na same ta ne sakamakon ilimin da nake dake da shi (ma'ana: ilimina ne ya bani, ba Allah ba)". Sannan saiYace:

---

[85] Godiya irin wacce ake kira **"Ash-shukr"** a larabce; it ace yayin da bawa ya sarrafa duk wata ni'imar da Allah I Ya baashi ta hanyar da Allah ɗin Ya yarda da shi. Idan dukiya ce ko ilimi ko wani ɓangare na mulki da sauransu, toh lallai ne bawa ya kiyaye haƙƙin Allah a ciki kuma Ya tsare dokokin Allah a yayin sarrafa su. Idan 'ya'ya ne, lallai ne ne bawa ya tarbiyyantar da su tarbiyyah ta addini. Wannan shi ake kira godiya a shari'ance, ba tsagwaran furta Hamdallah da fatar baaki kawai ba. **Allah Yasa mu dace.**

﴿أَوَلَمۡ يَعۡلَمۡ أَنَّ ٱللَّهَ قَدۡ أَهۡلَكَ مِن قَبۡلِهِۦ مِنَ ٱلۡقُرُونِ مَنۡ هُوَ أَشَدُّ مِنۡهُ قُوَّةٗ وَأَكۡثَرُ جَمۡعٗاۚ وَلَا يُسۡـَٔلُ عَن ذُنُوبِهِمُ ٱلۡمُجۡرِمُونَ﴾

Shin (wannan kangararren bawa) bai san cewa Allah ﷻ Ya halakar da waɗanda suka fi shi tsananin ƙarfi da kuma tarin dukiya ba a cikin ƙarnonin da suka shuɗe gabanin sa, kuma ba Ya tambayar masu laifi gameda (dalilin) aikata zunubansu (idan Ya tashi halakar da su, domin kuwa babu wani sauran hanzari garesu)" A can gaba sai Allah ﷻ Yace:

﴿فَخَسَفۡنَا بِهِۦ وَبِدَارِهِ ٱلۡأَرۡضَ فَمَا كَانَ لَهُۥ مِن فِئَةٖ يَنصُرُونَهُۥ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَمَا كَانَ مِنَ ٱلۡمُنتَصِرِينَ ٨١﴾

"Sai muka sanya ƙasa ta haɗiye shi daga shi har (katafaren) gidan nasa (wanda yake alfahari da shi). Ya kasance bashi da wasu tarin mutanen da za su iya taimakonshi (babu mai kuɓutar da shi daga wannan halaka) koma bayan Allah ﷻ, kuma shi bai kasance daga cikin masu (ikon) taimakon kawunansu ba"

Abinda ya zama wajibi akan duk wanda Allah ﷻ Ya bashi wani abu na jin daɗi a rayuwarsa ta duniya, shi ne ya gode wa Allah ﷻ (ya sarrafa wannan ni'ima ta hanyar neman yardarSa). Kar yayi butulci, kar yayi ɗagawa ko taƙama ko cika baki. Banda ƙoro kuma banda al-mubazzaranci.

Idan ka godewa Allah ﷻ, toh Zai albarkaci abin, kuma Zai Yarda da kai. Idan kuma mutum ya butulce, toh ko shakka babu ƙarshen lamarin ba zai masa daɗi ba. Allah dai Ya rufa mana asiri.

**Idan aka jarabci bawa da wata wahala ko ƙuncin rayuwa, da sauran ababenda zuciyarshi bata so:**

A irin wannan yanayi ana buƙata bawa yayi haƙuri, ya maida lamarinsa ga Allah ﷻ, Ya kuma nemi ladar wannan wahala a wajenSa.
Jarrabawa Sunnar Allah ﷻ ce. Kuma babu mai cin jarrabawar Allah Ta'ala sai wanda Yayi wa gamon katar. Allah Yasa mu cikin masu rabo.
Jarrabawa mai raɗaɗi (irinsu talauci da rashin lafiya da sauransu) ba ta daga cikin alamun da suke nuna wai Allah ﷻ ba Ya son bawanSa. Domin kuwaYa jarabci hatta manyan bayinSa ma da nau'ukan wahalhalu iri-iri a rayuwarsu.
Haka kuma samun ɗaukaka a duniya, da haɓakar tattalin arziki da sauransu, ba su suke nuna wai Allah ﷻ Yana son mutum sama da waɗanda basu samu ba.

Ayoyi da hadithai masu yawa sun tabbatar da cewa "Lallai Annabawa da Manzanni (Tsira da Amincin Allah su ƙara tabbata a garesu) su ne suka gamu da jarrabawa mafi tsanani daga cikin bayin Allah. Sannan kuma duk wanda ya bi tafarkinsu, toh zai samu jarrabawarsa gwargwadon iya koyin da yayi da su. Domin kuwa ana jarabtan bawa ne gwargwadon ƙarfin Addininsa."

Annabawa da Manzanni masu yawa jama'ansu sun ƙaryata su, an zage su, an musu izgilanci. Wasu an kore su daga gari, wasu an kama su an kulle a gidan yari anyi ta gana musu azaba, wasu ma kisan gilla akayi musu. Wasu daga cikin Annabawan kuma, tsantsar talauci da matsatsi sukayi ta fama da shi, akwai wanda ya kamu da rashin lafiya mai tsanani, akwai ma wanda ya shiga yanayinda har kifi ya haɗiye shi..
Amma duk hakan bai hana su ci gaba da tabbata akan wannan Tafarki madaidaici ba. Sun tsayu akai, sun jajirce

sun cigaba da kiran jama'arsu akai har Allah ﷻ Ya karɓi rayuwarsu.
Haka akeso mu ma mu zama. Mu nemi taimakon Allah ﷻ akan duk wata wahala ta rayuwa, da fatan Allah Ya hana ta tasiri wajen kautar damu hanya.

Waɗannan nau'uka na jarrabawa masu raɗaɗi suna da nasu amfani ga bawa matuƙar dai ya karɓi lamarin da zuciya guda (matuƙar ya yi haƙuri ya maida komi ga Allah ﷻ kuma ya nemi ladan hakan a wajenShi). Idan har yayi hakan, toh Zai yafe masa laifukansa kuma Zai bashi lada mai yawa.

Allah ﷻ Ya yi alƙawarin Zai ɗaukaka darajar masu haƙuri, Zai tabbatarda su akan Tafarkin shiriya, Zai Gafarta musu zunubansu, sannan kuma Zai musu Rahama a duniya da lahira.. Babban misali akan wannan shi ne (cikin Suratul-Baƙara, ayah ta 155 - 157) inda Allah ﷻ Yake cewa:

﴿ وَلَنَبۡلُوَنَّكُم بِشَيۡءٖ مِّنَ ٱلۡخَوۡفِ وَٱلۡجُوعِ وَنَقۡصٖ مِّنَ ٱلۡأَمۡوَٰلِ وَٱلۡأَنفُسِ وَٱلثَّمَرَٰتِۗ وَبَشِّرِ ٱلصَّٰبِرِينَ ﴾ [البقرة:١٥٥]

"Kuma lallai ne, za Mu jarabce ku da wani abu na tsoro da yunwa, da tawaya daga dukiya, da (asarar) rayuka da na 'ya'yan itace (amfanin gona). Don haka kayi bishara ga masu haƙuri"

﴿ ٱلَّذِينَ إِذَآ أَصَٰبَتۡهُم مُّصِيبَةٞ قَالُوٓاْ إِنَّا لِلَّهِ وَإِنَّآ إِلَيۡهِ رَٰجِعُونَ ﴿١٥٦﴾ ﴾ [البقرة:١٥٦]

"Su ne waɗanda suka kasance idan wata masifa ta same su, sais u ce: lalle mu daga Allah ﷻ muke, kuma lallai zuwa gareShi za mu koma"

﴿ أُوْلَٰٓئِكَ عَلَيۡهِمۡ صَلَوَٰتٞ مِّن رَّبِّهِمۡ وَرَحۡمَةٞۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُهۡتَدُونَ ﴾ [البقرة:١٥٧]

"Waɗannan lallai akwai Albarkatu da kuma Rahma (da za su riƙa sauka) akansu daga Ubangijinsu, kuma waɗannan su ne shiryayyu".

## Rashin Lafiya

Idan Musulmi ya kamu da rashin lafiya, wannan ciwo zai zama kaffarah gareshi (za a kankare masa laifinsa) matuƙar ya maida lamari ga Allah ﷻ, ya yarda da hukuncin Allah ﷻ, ya yarda cewa Allah ﷻ ne ya ɗora masa.

Allah ﷻ Yana ɗora wa bawa irin waɗannan nau'uka na jarrabawa ne, saboda Ya kankare masa zunubansa dasu, sannan kuma Ya bashi lada mai yawa, kuma Ya ɗaga darajarsa.

Manzon Allah ﷺ yana cewa: "Babu wani abinda zai sami Musulmi (a rayuwarsa) na yunwa ko rashin lafiya ko damuwa ko baƙin ciki ko wata cutarwa ko wani ƙunci –har ma da ƙayar da za ta soke shi- fahce Allah Ya kankare masa laifukansa da su[86]"

A cikin wani hadisin (riwayar Tirmidhiy daga Sahabi Abu-Huraira ؓ) Manzon Allah ﷺ yace: "Jarrabawa ba za ta gushe ba (tana sauka) ga mumini [da kuma mumina] a cikin jikinsa ko 'ya'yansa ko dukiyarsa, har sai gamu da Allah ﷻ (a lahira) babu wani laifi akansa (domin kuwa Zai kankare masa zunubansa sakamakon raɗaɗin da yayi ta ji a yayinda wannan jarrabawa ta same shi)".
Ashe idan mumini ya kamu da rashin lafiya, wannan wata dam ace da Allah ﷻ Yake bashi don ya tuba ya koma ga Allah, kuma ya samu ladan haƙuri, sannan kuma ciwon ya zama kaffara gareshi gameda zunuban da ya aikata. Shi yasa

[86] Bukhari (**5643**), da Muslim (**2573**) Daga Abu-huraira t da Abu-Sa'id Al-khudri ؓ

Manzon Allah ﷺ ya kasance idan yaje duba mara lafiya musulmi, daga cikin addu'o'inda yake masa akwai:

لَا بَأْسَ طَهُورٌ إِن شَاءَاللَّهُ

"Babu laifi, ciwon naka mai tsarkakewa ne (daga zunubanka) in Allah Ya Yarda[87]"

**Haƙuri gameda rasuwar ɗa ko ɗiya:**

Idan bawa yayi haƙuri ya daure kuma ya nemi lada gun Allah ﷻ a yayinda ya rasa ɗa ko ɗiya, toh hakan ma yana daga cikin hanyoyin samun Gafarar Allah (bayan ɗumbin ladan da zai samu sakamakon hakan) insha'Allah.

Manzon Allah ﷺ yace: "Babu wasu musulmi biyu (miji da matarsa) da za su rasa 'ya'ya ƙanana har guda uku (kuma suyi haƙuri su mayarda lamarinsu ga Allah ﷻ) fahce an Gafarta musu[88]"

A wata riwayar ma, Manzon Allah ﷺ cewa yayi: "Duk wanda ya nemi lada (haƙurinda yayi) gameda rashin har ('ya'ya) uku daga cikin tsatsonsa, toh zai shiga Aljannah (sakamakon hakan)". Sai wata mace tace: "Har da mai biyu ma (Ya Manzon Allah)?" Yace mata: "Har mai biyu ma[89] (shi ma zai samu irin wannan sakamako)".

Wasu hadisai ma sun tabbatar da cewa hatta wanda ya rasa ɗa guda ma zai samu irin wannan sakamako

---

[87] Bukhari (3616) daga Abdullahi ɗan Abbas Allah Ya ƙara musu Yarda (shi da mahaifin nashi).

[88] Nasa'i (Hadithi na1874 ) daga Sahabi Abu-Dharrin Al-Ghifariy ﷺ

[89] Musnad na Imamu Ahmad (Hadithi na 27429) Daga Sayyida Ummu-Sulaim (Mahaifiyar Anas ɗan Malik) Allah Ya ƙara musu yarda.. Akwai ma'anar wannan hadithi cikin Sahihul-Bukhari da kuma Sahih Muslim a wurare daban daban.

insha'Allah. Da sharaɗin dai za ayi haƙuri tun a farkon fari, a mayar da lamari ga Allah ﷻ, kuma a nemi ladan wannan haƙuri da juriya awajenSa. Toh idan har bawa ya rasa ɗansa kuma yayi haƙuri ya maida komai ga Ubangijinsa, Allah ﷻ Zai ce wa Mala'iku: "Ku gina wa bawa Na gida a cikin Aljannah, kuma ku sanya wa gidan suna بَيْتُ الْحَمْدِ (gidan godiya, wanda sai masu godiya ga Allah akan komai ne kaɗai zasu sami irinta)[90]"

Manzon Allah ﷺ yace: "Babu wani wata kyautar da za baiwa wani (daga cikin bayi) wacce take cike da Alkhairi kuma wadatacciya irin kyautar haƙuri[91]".

Saboda girman matsayin haƙuri, babu wanda yasan yawan ladan da bawa zai samu idan yayi haƙuri sai Allah ﷻ kaɗai.

A cikin Suratuz-Zumar (ayah ta **10**) Allah ﷻ Yana cewa:

﴿إِنَّمَا يُوَفَّى ٱلصَّٰبِرُونَ أَجْرَهُم بِغَيْرِ حِسَابٍ ﴿١٠﴾﴾ [الزمر:١٠]

"Masu haƙuri ne kaɗai ake cika musu ladan sub a tare da ƙididdiga ba"

Renon 'ya'ya mata, da kuma kyautata Tarbiyyarsu har su girma.

Wannan ma yana daga cikin muhimman hanyoyin samun Gafarar Allah ﷻ, da RahamarSa da AljannarSa.

Manzon Allah ﷺ yace: "Duk wanda aka jarabce shi da (renon wani adadi daga cikin) waɗannan 'ya'ya mata, kuma

[90] Tirmizi **(1021)** daga Abu-Musa Al-Ash'ari ﷺ. Hadithi ne mai kyau. Duba As-Sahiha (**1408**).

[91] Bukhari **(6470)** da Muslim **(1053)** daga Sahabi Abu-Sa'id Al-khudri ﷺ

ya kyautata musu (tarbiyyah), toh za su kasance gareshi shamaki tsakaninsa da wuta (a gobe ƙiyamah)[92]".
A wata riwayar Imam Ahmad da Ibnu Majah kuma, Manzon Allah ﷺ cewa yayi: "Duk wanda ya kasance yana da 'ya'ya mata har uku, kuma yayi haƙuri (ya daure ya tarbiyyantar dasu) ya ciyar dasu ya shayar dasu ya kuma tufatar dasu daga abinda ya mallaka; toh za su kasance shamaki gareshi daga wuta a ranar tashin ƙiyamah".

## Daurewa a kyautata Ibada a yayinda ake cikin tashe-tashen hankula da kashe-kashe

Sau da dama (musamman a wannan zamani) ana samun tashe-tashen hankula a yankunan da muke yaruwa. Mutane za su lalace suyi ta ɓarna, kuma babu mai hana su. Za a wayi gari ana ta'addanci iri-iri. Masu Mulki su kangare suyi ta cin zalin talakawansu. Kuma sau da dama babu waɗanda aka fi cutarwa a irin waɗannan lokuta irin masu riƙo da addini.

Toh idan bawa yayi haƙuri ya daure ya jajirce ya tsaya ya bauta wa Allah a irin wannan lokaci, toh hakan yana daga cikin hanyoyin samun Gafarar Allah ﷻ.
Domin kuwa Manzon Allah ﷺ yana cewa: "Bautar Allah acikin lokaci na haraj (wato kashe-kashe da yaƙe-yaƙe) kamar hijira ce zuwa gareni[93]".
Sanannen abu ne kuma Hijira ma tana shafe abinda ya gabaceta na laifuka, kamar yadda Imam Muslim ya ruwaito (hadisi na 121) daga Sahabi Abdullahi ɗan 'Amru ɗan As, Allah ƙara Yarda dasu baki ɗayansu.

---

[92] Bukhari **(5995),** Muslim **(2629),** Dukkansu daga Nana A'isha Allah Ya ƙara Yarda da ita.
[93] Sahih Muslim (Hadithi na 2948) daga Sahabi Ma'aƙili ɗan Yasaar ﷺ

Ko shakka babu idan har bawa ya jajirce ya tsaya akan gaskiya a irin lokacinnan da mutanen banza sukayi yawa hatta cikin al’ummar Musulmi, toh zai samu babbar daraja awajen Allah ﷻ. Allah ﷻ Zai bashi ladan haƙuri, kuma Zai sanya shi cikin bayinSa nagari (masu rabauta a duniya da lahira).
Shi yasa a cikin Suratu-Hud (ayah ta 11) Allah ﷻ Yake cewa:

﴿إِلَّا ٱلَّذِينَ صَبَرُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُم مَّغۡفِرَةٞ وَأَجۡرٞ كَبِيرٞ ١١﴾

“Sai waɗanda sukayi Imani kuma suka aikata ayuka na ƙwarai, waɗannan kam suna da Gafara da kuma Lada mai Girma”

Haka kuma idan bawa yayi haƙuri saboda wata cutarwar da akayi masa (aka ci masa mutunci, akayi masa izgili ko ƙage da yarfe da ƙazafi da kuma ɓata suna) ba don komai ba sai don kaɗai ya yi riƙo da addin Allah, Toh hakan yana daga cikin hanyoyin samun Gafarar Allah, da AljannarSa.

Allah ﷻ Yace irin bayin nan naShi waɗanda aka cutar dasu (akayi ta musu izgilanci a duniya sakamakon riƙon su da addini), toh zai saka musu a lahira saboda haƙurinda sukayi. Zai saka musu da Aljannah, kuma Zai goranta wa masu yi musu izgili (bayan su kuma masu izgilin suna cikin wuta).
Acikin Suratul-Muminun (ayah ta 109 - 111) Allah ﷻ Yana cewa:

﴿إِنَّهُۥ كَانَ فَرِيقٞ مِّنۡ عِبَادِي يَقُولُونَ رَبَّنَآ ءَامَنَّا فَٱغۡفِرۡ لَنَا وَٱرۡحَمۡنَا وَأَنتَ خَيۡرُ ٱلرَّٰحِمِينَ ١٠٩

“Lallai wani kaso daga cikin bayiNa sun kasance suna cewa Ya Ubangijin mu munyi imani, saboda haka Ka Gafarta

mana kuma Kayi mana Rahma, domin kuwa Kai ne Mafi Jinƙan Masu Jinƙai.

فَٱتَّخَذۡتُمُوهُمۡ سِخۡرِيًّا حَتَّىٰٓ أَنسَوۡكُمۡ ذِكۡرِي وَكُنتُم مِّنۡهُمۡ تَضۡحَكُونَ ﴿١١٠﴾

Sai ku kuma kuka riƙe su ababen yiwa izgili (kuna ta tsokanarsu saboda sunyi riƙo da addini), har (suka shagaltar daku) suka mantar daku ambato Na, kun kasance kuna ta musu dariya (saboda kawai sunyi imani).

إِنِّي جَزَيۡتُهُمُ ٱلۡيَوۡمَ بِمَا صَبَرُوٓاْ أَنَّهُمۡ هُمُ ٱلۡفَآئِزُونَ ﴿١١١﴾

Toh lallai Ni Na saka musu yau (Na basu Aljannah) saboda haƙurinda sukayi (akan cutarwar da kukayi ta musu a duniya), lallai kuwa su ɗinnan su ne masu babban rabo". Shi ma wanda akayiwa ƙazafi don neman ganin bayansa saboda kawai ya yi riƙo da addini, Allah ﷻ Ya yi masa alƙawarin Gafara da kuma girmamawa. Ya faɗi hakan ne a cikin Suratun-Nur (ƙarshen ayah ta **26,** cikin ayoyinda Ya wanke Uwar mu Nana-A'isha daga ƙazafinda munafukai sukayi mata[94]).

Allah ﷻ Yace:

﴿أُوْلَٰٓئِكَ مُبَرَّءُونَ مِمَّا يَقُولُونَۖ لَهُم مَّغۡفِرَةٞ وَرِزۡقٞ كَرِيمٞ ﴿٢٦﴾﴾

"Irin waɗannan su ne waɗanda ake barrantarwa daga abinda (masharranta) suke faɗa. Suna kuma da Gafara da kuma wani irin Arziki na girmamawa"

[94] Hadisin wannan ƙazafi ya zo cikin littatafan hadisi da kuma sirah masu yawa. Babban misali akan wannan, shi ne hadisi na **4141** cikin Sahihul-Bukhariy, hadithin Nana-A'isha ɗin (ita da kanta ta bayar da wannan labara). Waɗanda suka kitsa wannan ƙazafi dai sunyi ne saboda cin mutunci ga Manzon Allah ﷺ gameda iyalansa. Kuma abin takaici, 'yan shi'a suna ci gaba da zargin ta da wannan laifi, bayan Allah ﷻ Ya wanke ta a cikin Al-Kur'ani. Kuma daga baya su saɗaɗo su ce wai su ma suna ƙaunar Manzon Allah ﷺ. wallahi ƙarya sukeyi. Su cikakkun maƙiya ne ga Allah da ManzonSa da kuma AddininSa.

Idan aka zartar da haddi (irin na shari'a) akan bawa saboda wani laifinda ya aikata:
Haddin da akayi wa bawa yana shafe wannan laifinda yayi. Zai zamto kaffarah gareshi, ta yadda ba za ayi masa uƙuba akan wannan laifin ba a lahira. Saboda haka haddi ma yana daga cikin hanyoyin samun Gafarar Allah ﷻ kenan.
Za mu ga shaidar hakan a cikin hadisin wata matar da aka tsayar mata haddin rajamu (jifa da tsakuwa sakamakon an kama ta da laifin zina alhalin ta taɓa aure) a zamanin Manzon Allah ﷺ.
Bayan ta mutu ai Manzon Allah ﷺ ne yayi mata Sallah. A lokacinda ya shige gaba don ya jagoranci Sallar ma, har Sayyiduna Umar ؓ yake cewa: "Ya Ma'aikin Allah ta yaya kuma (kai da kanka) za ka sallaci wannan mata alhali kuma zina tayi?" Sai Manzon Allah ﷺ yace masa: "Haƙiƙa ta yi wani irin tuba wanda ko da za raba wa mutum saba'in daga cikin mutanen wannan birni na Madinah, da zai ishe su[95]"

**Fitintinun Kabari** (Allah Ya tsare mu)
Daga cikin Musulmi ma akwai waɗanda za a fitinesu a cikin ƙaburburansu. Za a fitini kowa daga cikinsu ne gwargwadon aikinsa, sai wanda Allah Ya kuɓutar dashi kawai.
Manzon Allah ﷺ yace Shahidi ne kaɗai ba za a fitine shi ba a cikin ƙabarinsa[96]. Har ma yace: "Da ace akwai ɗaya (daga cikin mutane) da zai kuɓuta daga matsa irinta ƙabari, da kuwa (Sahabi) Sa'adu ɗan Mu'azu ؓ ne zai tsira[97]"

---

[95] Muslim (Hadisi na 1696) daga Sahabi Imran ɗan Husain ؓ.
[96] Imam An-Nasa'iy (hadisi na **2053**). Yana ma cikin littafin At-Ta'liƙ ar-Raghib (**2/197**)
[97] Imam Ahmad, daga Abdullahi ɗan Umar (Allah Ya ƙara yarda da su). Shaykh Albaniy yace hadisin ya inganta (duba As-Saheeha, hadithi na **1695**)

Mutane sun kasu har wajen kashi biyar daban-daban a cikin rayuwar su ta ƙabari:

a. Akwai waɗanda su kam azaba ce zallah iri-iri zasu yi ta sha tun daga cikin ƙabari har zuwa lahira, kuma za su dawwama a wuta.. Waɗannan su ne Kafirai da kuma Munafukai.
b. Akwai kuma waɗanda su ma za su sha azabah a cikin ƙabari, kuma a lahira za su shiga wuta su daɗe a ciki. Amma su ba za su dawwama a cikinta ba, saboda ba akan kafirci suka mutu ba. Illa iyaka za a musu uƙuba ne sakamakon zunubansu masu yawa sosai (waɗanda har suka mutu basu tuba sun daina ba), kuma ba'a ga damar yafe musu ba. Daga baya za a fitar dasu daga wutar, a wanke su, a shigar dasu Aljannah.
c. Akwai wanda ni'ima zai ta sha tun daga farko har ƙarshe a ƙabarinsa. Wani ma ko tambaya ba za ayi mas aba. Idan kuma yaje lahira zai shige totar zuwa Aljannah. Allah Yasa mu ne.

d. Akwai wani kuma matsa guda kawai za ayi masa na wani ɗan lokaci, daga nan shi kenan, babu wata fitina. Kuma a lahira Aljannah zai shiga.
e. Akwai kuma wanda za ayi masa azaba a Kabarinsa na wani lokaci don a wanke shi a tsaftace shi daga zunubansa.. Daga baya sai a ɗauke wannan azabar, a sanyaya masa a musanya masa da ni'ima.. Irin waɗannn ne babban Malami (Shaykhul-Islam) Ibnu Taymiyyah Rahimahullah yake cewa: "Abindfa yake faruwa a cikin ƙabari na fitina da shan matsa da kuma firgici da razani, waɗannan suna cikin ababenda ake kankare laifuka da su[98]"

[98] Fataawa (juz'i na **7**, shafi na **308**), bugun Daarul-wafaa'i, Tahƙiƙi da Takhrijin Aamir Al-Jazzar da kuma Anwar Al-baaz

Allah Ya tsare mu daga fitina da kuma azabar ƙabari, da kuma azabar wuta. Allah Yasa Aljannah ce makomar mu a gobe Kiyamah.

***

### (Hanya ta Takwas)

## Addu'ar Mumini ga ɗan-uwansa Mumini

### (musamman ma ida ya roƙa masa Gafarar Allah)

Allah ﷻ Yana karɓar addu'ar da mumini yayi wa ɗan-uwansa mumini, musamman ma wacce akayi masa a bayan idonsa (ba tareda ya sani ba).

Malamai suka ce ko wanne Musulmi yana da wasu haƙƙoƙi akan ɗan-uwansa Musulmi. Daga cikin waɗannan haƙƙoƙin dai, dole ne a roƙa masa gafara (sawa'un yana raye ne ko bayan ya mutu).

Akwai ayoyin Kur'ani da ingantattun hadithai da suka tabbatar da wannan ƙa'idar da suka ambata. Daga cikinsu akwai faɗin Allah ﷻ (akan harshen bayinSa na ƙwarai masu yiwa magabatansu addu'a):

﴿رَبَّنَا ٱغۡفِرۡ لَنَا وَلِإِخۡوَٰنِنَا ٱلَّذِينَ سَبَقُونَا بِٱلۡإِيمَٰنِ وَلَا تَجۡعَلۡ فِي قُلُوبِنَا غِلّٗا لِّلَّذِينَ ءَامَنُواْ رَبَّنَآ إِنَّكَ رَءُوفٞ رَّحِيمٌ ١٠﴾ [الحشر: ١٠]

"Ya Ubangijinmu Ka gafarta mana, mu da 'yan-uwanmu da suka riga mu da imani (bayinKa na ƙwarai waɗanda suka shuɗe). Kada Ka sanya wani ƙulli (na ƙiyayya da gaba) a cikin zukatanmu gameda waɗanda sukayi imani. Ya Ubangijinmu lallai Kai ne Mai Tausayawa kuma Mai Jinƙai"

Sannan kuma sanannen abu ne cewa duk wani Musulmin da ya mutu, toh dole ne sauran 'yan-wansa Musulmi su yi masa jana'iza kuma su binne shi. Wannan haƙƙi ne tabbatacce a cikin shari'ar Musulunci.

Kuma Manzon Allah ﷺ Ya tabbatar mana cewea matuƙar Musulmi ya sauke wannan hakki, toh fa yana da ɗumbin lada wajen Ubangiji ﷻ.
Yace: "Idan har bawa ya halarci Sallar jinaza ta ɗan-uwansa Musulmi, toh yana da lada kwatankwacin ƙiraɗi[99] guda. Idan kuma ya tsaya ya raka gawar har aka binne ta, toh yana da Kiraɗi biyu na lada"
Sannan kuma wannan Sallah da za ayi wa mamaci, tana ma da amfani gareshi sosai. Saboda tana daga cikin hanyoyin samun gafara gareshi.
Manzon Allah ﷺ yana cewa: "Babu wani mamaci (cikin Musulmi) da wani kaso na al'ummar Musulmi za su sallace shi su kimanin mutum ɗari, kuma kowanne daga cikinsu

[99] Malamai suka ce Kalmar **Kiraɗi** yana nufin: tsauni mai girma, wanda ƙaraminsa ma ya kai kamar girman dutsen uhudu (duba Musnad na imam Ahmad, hadisi na **10079**, daga Sahabi Abu-Huraira ﷺ).

yana neman a bashi ceton sa, fahce sai an basu ceton nashi[100]".

A wata riwaya kuma[101], Manzo ﷺ cewa yayi: "Babu wani mutum musulmi da zai mutu, kuma a samu har mutum arba'in waɗanda basu shirka su tsaya su sallaci gawarsa fahce sai Allah ﷻ Ya basu ceton sa (zai gafarta masa sakamakon wannan addu'ar da sukayi masa, matuƙar shi ɗin ma ba ya shirka)".

Allah ﷻ Zai yafe masa duk laifukanda yayi masa. Sauran abinda yake tsakaninsa da mutane kuma, wannan shi dasu. Sai mu kiyaye sosai gameda haƙƙin mutane.

Shi yasa ma malamai suka ce yana da kyau mu riƙa rubutawa mu ajiye, saboda wata rana. Amma fa lallai ne muyi ƙoƙarin biya da kanmu ne. Idan kuma hakan bai samu ba har lokaci yayi, toh magadanmu za su sani ta hanyar abinda muka rubuta muka ajiye.

Mu da Allah ﷻ Yasa muke raye a halin yanzu, ya kamata mu sani ba fa iyawar mu ba ce. Dole wata rana mu ma za mu mutu. Kuma na tabbata kowa daga cikinmu yana buƙatar a riƙa sanya shi cikin addu'a bayan ya mutu. Toh yana da kyau mu ma yawaita roƙa wa mamatanmu Gafarar Allah ﷻ (musamman iyayenmu da sauran makusanta).

Mu gaggauta biya musu basussukan da ake binsu don su samu sauƙi. Tabbas yin hakan yana daga cikin kayutatawa garesu a matsayinsu na waɗanda suka riga suka rasu.

Idan ma akwai bashin azumi akansu (musammanma na bakance) mu daure mu rama musu. Idan ma mun samu ikon zuwa muyi musu aikin Hajji ko Umrah (ko dukka biyun), toh muyi musu (bayan mu munyi namu). Waɗannan dukkansu suna cikin kyautatawa garesu. Kuma zasu amfana

---

100 Muslim (Hadithi na 947) daga Sayyida Nana A'isha da Anas ɗan Malik, Allah Ya ƙara musu yarda.

101 Muslim (Hadithi na 948) daga Sahabi Abdullahi ɗan Abbas Allah Ya ƙara musu Yarda.

da hakan sosai insha'Allah. Mu ma kuma za mu samu lada insha'Allah.

Babban abinda yafi dacewa dai shi ne; kowa ya dage yayiwa kansa da kansa. Wannan shi yafi dacewa.
Kar mutum ya tsaya wai ya dogara da abinda magada zasu yi masa bayan ya mutu. Domin kuwa duk yadda za su tuna da kai, ba za su tuna ka kamar yadda suke tuna kawunansu ba. Kuma da ma ba akan komai da komai za su iya maka wani abu ba (sai cikin wasu 'yan taƙaitattun al'amura ne kawai). Duk kuma abinda za sum aka ɗin ma, toh fa wakilci ne kawai, ba zai kai abinda kai za ka yiwa kanka da kanka ba. Bahaushe kuma yace zuwa da kai ya fi saƙo.
Saboda haka mu dage wajen ganin mun amfana da wannan damar rayuwa da Allah ﷻ Ya bamu kafin mu ma ta kuɓce mana. Domin kuwa babu makawa za ta ƙare.
Allah Ya rufa mana asiri, kuma Yasa mu cika da imani.

***

## (Hanya ta Tara)

## Ceton Manzon Allah ﷺ a gobe Kiyama

Ceton Manzon Allah ﷺ gaskiya ne. Imani da shi kuma dole ne. Babu mai musun hakan sai mara rabo.
Ceton da Allah ﷻ Yayi izni, kala biyu ne (ɗaya Ya keɓance ManzonSa Muhammadu ﷺ shi kaɗai, ɗaya kuma shi da sauran manyan abyin Allah):

1. An keɓance Manzon Allah ﷻ wajen bashi ceton duk bayi (mutane da aljanu), don ayi hisabi a baiwa kowa sakamakon abinda ya aikata a rayuwarsa ta duniya.
   -Sannan kuma an keɓance shi da ceton 'yan Aljannah ma. Su ma zai cece su a gobe ƙiyamah. Domin kuwa dole sai ya ƙwanƙwasa ƙofar Aljannah tukunna kafin a buɗe wa bayi su shiga.

-Haka nan kuma akwai ceton sa ga baffan sa Abu-Talib. Domin an rage masa raɗaɗin azabar da ake masa a cikin wuta, sakamakon irin matsayinsa wajen Manzon Allah ﷺ. Wannan dai shi ne iyaka amfanin da zai masa, tunda ya mutu bai musulunta ba. Allah Yasa mu cika da imani.

2. Sannan akwai ceton da aka bashi amma ba a keɓance shi shi kaɗai ba. Hatta Mala'iku da sauran Annabawa da Manzanni da kuma sauran salihan bayi ma za a basu irin wannan ceto na biyu; shi ne ceton da za ayi wa masu laifi (wasu za a cece su daga shiga wuta, wasu kuma sai an shigar da su wuta an fara musu azaba na wani lokaci sai a bada iznin cetonsu ga masu ceto daga baya).

Sannan kuma ceto yana da sharuɗa guda biyu ne, waɗanda dole sai sun cika kafin ya tabbata.

a. Dole sai wanda Allah Yayi wa izni ne kaɗai zai yi ceto.
b. Kuma dole sai wanda Allah ﷻ Ya ga dama kaɗai za a ceto daga cikin bayinSa (kuma a lokacinda Ya ga dama).

Ya tabbata cikin littafin Imam At-tirmidhi, Manzon Allah ﷺ yana cewa: "Akwai ceto na ga ma'abota kaba'irai (manyan laifuka) daga cikin Al-ummah ta[102]"
Idan fa akace masu aikata kaba'irai anan; ana nufin masu aikata sauran kaba'irai ne (banda shirka[103]a ciki). Domin shi kam duk wanda ya mutu bai tuba daga gareshi ba, toh babu wani ceton da zai amfane shi. Allah ﷻ yace:

﴿فَمَا تَنفَعُهُمْ شَفَٰعَةُ ٱلشَّٰفِعِينَ ۝٤٨﴾ [المدثر:٤٨]

"Saboda haka ceton masu ceto ba zai amfane shi ba (saboda ya mutu bai tuba ba daga kafircinsa ba)"

---

[102] Tirmidhi ne ya ruwaito shi, daga Sahabi Jabir ɗan Abdullahi, da kuma Anas ɗan Malik, Allah Ya ƙara musu Yarda su dukansu.
[103] Duba Kitabut-Tauhid na Al-Imam Ibnu-khuzaimah (Allah Ya Gafarta masa).

Don haka dai ceton da Manzao ﷺ ya ambata a cikin wannan hadisi, yana nufi cetonsa ga ma'abota kaba'irai ne waɗanda suka mutu basu tuba ba, sannan kuma babu shirka a cikin duk laifukan nasu. Toh su ne wannan ceto zai shafa Insha'Allah. Sahabi Auf ɗan Malik ﷺ yace wata rana ya ji Manzo ﷺ yana cewa: "Wani mai tahowa ya taho gareni daga gun Ubangijina, ya bani zaɓi tsakanin (ko dai) a shigar da rabin Al-ummah ta Aljannah ko kuma a bani ceto. Sai na zaɓi a bani ceton nan. Kuma shi (ceton) zai kasance ne ga wanda ya mutu (daga cikin Al'ummah ta) alhalin ba ya haɗa Allah da komai a cikin bauta"[104].

Munyi Imani da ceton Manzon Allah ﷺ. Kuma muna roƙon Allah ﷻ Ya arzuƙta mu da samun cetonsa a gobe Kiyamah.

***

## (Hanya ta Goma)

# Afuwar Allah ﷻ Da kuma RahamarSa

## (Ga wanda Ya ga dama cikin bayinSa)

Daga cikin Yalwatacciyar Rahamar Allah ﷻ, akwai wasu daga cikin bayinSa waɗanda Zai Yafe musu a gobe ƙiyamah, tareda kuma sun je sun same Shi da tarin zunubai, amma a cikin laifukan nasu dai babu shirka. Domin kuwa Allah ﷻ ba Ya yafewa duk wanda ya mutu bai tuba daga shirka ba.
A cikin Suratun-Nisa'i ayah ta **48** Allah ﷻ Yana cewa:

[104] Musnad na Imaam Ahmad (Hadithi na 24023), Tirmidhi (Hadithi na 2441), Ibnu Majah (Hadithi na 4317). Dukkansu daga Sahabi Auf ɗan Malik ﷺ.

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَغْفِرُ أَن يُشْرَكَ بِهِۦ وَيَغْفِرُ مَا دُونَ ذَٰلِكَ لِمَن يَشَآءُ ۚ وَمَن يُشْرِكْ بِٱللَّهِ فَقَدِ ٱفْتَرَىٰٓ إِثْمًا عَظِيمًا ﴾

"Lallai Shi fa Allah ba Ya Gafarta wa idan aka yi masa shirka (kuma har aka mutu aka ba'a tuba ba), amma Yana yafe wa (idan aka aikata) koma bayan wannan ga wanda Ya ga dama. Toh duk wanda Ya haɗa Allah da wani a yayin bauta, haƙiƙa ya ƙirƙiri laifi mai girma".
A can gaba kuma (aya ta 116), sai Ya rufe ayar da cewa:

﴿ وَمَن يُشْرِكْ بِٱللَّهِ فَقَدْ ضَلَّ ضَلَٰلًۢا بَعِيدًا ﴾ [ النساء:١١٦ ]

"…Kuma duk wanda ya haɗa Allah da wani a yayin bauta, haƙiƙa ya ɓata ɓata mai nisa"
Saboda haka ma ya haramta Aljannah kwata-kwata ga wanda Ya mutu yana shirka. Haka Ya faɗa a can cikin Suratul-Ma'idah (a ƙarshen ayah ta 72) inda Yake cewa:

﴿ إِنَّهُۥ مَن يُشْرِكْ بِٱللَّهِ فَقَدْ حَرَّمَ ٱللَّهُ عَلَيْهِ ٱلْجَنَّةَ وَمَأْوَىٰهُ ٱلنَّارُ ۖ وَمَا لِلظَّٰلِمِينَ مِنْ أَنصَارٍ ﴾

"Lallai duk wanda ya haɗa Allah ﷻ da wani a wajen bauta (kuma har ya mutu bai tuba ba), toh haƙiƙa Allah ﷻ Ya haramta mishi Aljannah, kuma makomarsa it ace wuta, kuma waɗannnan azzalumai (masu shirka) basu da wasu mataimaka (babu wanda zai taimake su ya kyɓutar dasu daga wannan madawwamiyar azaba)"

Saboda haka babban sharaɗin samun Gafara ta Allah ﷻ (a ko da yaushe) shi ne kuɓuta daga shirka. Mannzon Allah ﷺ yace: Allah ﷻ Yana cewa: "Duk wanda ya same Ni da zunubai (masu yawa, ko da kuwa yawan su ya kai) kusan yawan ƙassai, amma kuma ya kasance ba ya haɗa ni da

komai wajen bauta, toh Ni kuma Zan zo masa da kwatankwacin ta na gafara[105]".

Akwai waɗanda Allah ﷻ Zai Yafe musu tun a filin hisabi. Zai rufa musu asiri Yace su shige kawai, tareda kuma suna da zunubai masu yawa, amma da Yake babu shirka aciki sai Yayi musu afuwa.

Su ne waɗanda Allah ﷻ Zai musu hisabi mai sauƙi inji Manzon Allah ﷺ.

Hadithi ya tabbata kan wannan al'amari a cikin Musnad na Imamu Ahmad, Hadithi na **6944**, daga Sahabi Abdullahi ɗan Amru ɗan As Allah Ya Kara musu yarda (shi da mahaifin nashi dukka).

Akwai kuma waɗanda za su shiga wuta sakamakon zunzurutun zunubansu, kuma duk waɗanda aka baiwa izinin yin ceto sunyi sun gama amma banda su cikin waɗanda za a ceto ɗin, sai daga baya Shi kuma Allah ﷻ Yayi musu afwa Ya fitar dasu daga wutar, Ya wanke su da wani ruwa mai suna **Ma'ul-Hayati** (ruwan rayuwa), sannan Ya shigar da su Aljannah. Su ne ma talakawan Aljannah, kamar yadda ingantattun hadithai masu yawa suka tabbatar.

Akwai ma waɗanda za a fara ajiye su akan wasu tuddai dake tsakanin Aljannah da wuta (inda ake kira **Tozon la'arafi** a hausance). Za a ajiye su a wajen su zauna na wani lokaci (suna ganin Aljannah kuma suna ganin wuta, amma basu shiga kowacce daga ciki ba) har zuwa wani lokacinda Allah Ya ga dama, sannan daga ƙarshe su ma Ya shigar dasu aljannah. Allah ﷻ Ya bada labarin waɗannan bayi naShi a cikin Suratul-A'araf (wajen ayah ta **46** zuwa **49** haka).

---

[105] Sahih Muslim (Hadithi na 2687) daga Sahabi Abu-Dharrin Al-Ghifaariy ؓ

Ba don komai yasa duk wannan yake faruwa ba, sai don kasancewar da ma can Allah ﷻ ba Ya nufin Ya azabtar da bayinSa. Ba Ya kuma ɗora wa bawa sai abinda shi bawan zai iya ɗauka.
Babu wanda za a azabtar a lahira fahce shi da kansa ya tabbatarwa kansa cewa lallai ya cancanci hakan. Domin kuwa shi ya jawo wa kansa. Saboda haka dole yayi kuka da kansa, ba da wani ba.
Shi yasa a wani Hadithi Manzon Allah ﷺ yace: Allah ﷻ Yana cewa: "Ya ku bayi na! Ku sani duk ayukan nan naku dai (da kuke aikatawa) ina nan ina kiyaye muku su (babu abinda zai salwanta daga ciki). Sannan zan cika wa kowa su (ta hanyar bashi littafin ayukansa a lahira). Saboda haka duk wanda ya sami Alkhairi, toh ya godewa Allah ﷻ (saboda Shi ne Ya datar dashi da wannan aiki nagari). Wanda kuma ya samu kishiyar hakan, toh kar ya zargi kowa sai kansa (saboda shi ya zaɓa wa kansa bin tafarkin shaiɗan)[106]"
Saboda haka duk wanda ya shiga wuta a gobe ƙiyamah, toh fa shi ya saya wa kanshi wannan azabah da kuɗinsa. Amma Allah ﷻ kam, ba Ya nufin wata wahala da bayinSa. Allah ﷻ Yace:

﴿يُرِيدُ ٱللَّهُ بِكُمُ ٱلۡيُسۡرَ وَلَا يُرِيدُ بِكُمُ ٱلۡعُسۡرَ﴾ [البقرة:١٨٥]

"Allah ﷻ Yana nufinku da sauƙi, ba Ya nufinku da wahala"

Saboda haka ne ma Ya sauƙaƙa mana nau'ukan Ibadah Ya kuma yawaita mana su, Ya sanya wahala cikin ayukan saɓo, Ya yawaita mana hanyoyin samun RahamarSa, Ya buɗe mana ƙofofi masu yawa na tsira saboda tausayinmu da Yakeyi.

- Yana ruɓanya mana Lada idan muka aikata wani aiki nagari..

[106] Sahih Muslim (Hadithi na 2577) daga Sahabi Abu-Dharrin Al-Ghifaariy ؓ

- Yana Gafarta mana zunubanmu[107]
- A kullum kuma Yana kiranmu zuwa ga neman GafararSa, don mu rabauta a duniya da lahira.

A cikin Suratuz-Zumar (daga ayah ta 53 har zuwa ta 55) Allah ﷻ Yana cewa:

﴿ ۞ قُلْ يَٰعِبَادِىَ ٱلَّذِينَ أَسْرَفُوا۟ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمْ لَا تَقْنَطُوا۟ مِن رَّحْمَةِ ٱللَّهِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ يَغْفِرُ ٱلذُّنُوبَ جَمِيعًا ۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلْغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ﴿٥٣﴾ ﴾

Allah ﷻ Yana cewa: "(Ya Muhammadu) kace musu (Allah ﷻ Yana cewa): Ya ku bayi na waɗanda suka yi ɓarna kan rayukansu (suka zalunci kawunansu ta hanyar aikata laifuka, sakamakon haka suka tara zunubai masu yawa)! Toh kada ku yanke ƙauna daga Rahamar Allah (kada ku ɗebe tsammani). Domin kuwa lallai Allah ﷻ Yana Gafarta (wa bawa) zunubai gaba ɗaya. Saboda lallai Shi, Shi ne kaɗai mMai gafara, kuma Mai Jinƙai"

A cikin ayah ta gaba sai Ya cigaba da cewa:

﴿ وَأَنِيبُوٓا۟ إِلَىٰ رَبِّكُمْ وَأَسْلِمُوا۟ لَهُۥ مِن قَبْلِ أَن يَأْتِيَكُمُ ٱلْعَذَابُ ثُمَّ لَا تُنصَرُونَ ﴿٥٤﴾ ﴾

"Kuma ku mayar da lamari zuwa ga Ubangijinku, kuma ku miƙa wuya gareShi (kada ku aikata abinda Ya hane ku, kuma kar ku saɓa wa umurnin Sa), tun kafin azaba ta zo muku, sa'annan kuwa ba za a taimake ku ba"

Sanna kuma sai Yace:

﴿ وَٱتَّبِعُوٓا۟ أَحْسَنَ مَآ أُنزِلَ إِلَيْكُم مِّن رَّبِّكُم مِّن قَبْلِ أَن يَأْتِيَكُمُ ٱلْعَذَابُ بَغْتَةً وَأَنتُمْ لَا تَشْعُرُونَ ﴿٥٥﴾ ﴾

[107] Ta hanyar Tuba da Istighfari, ko wani aiki nagari, ko wata hanya ta daban cikin waɗanda aka ambata a wannan ɗan littafin (da sauran manyan littattafai na manyan Malamai, Allah Ya Saka musu da Alkhairi).

"Kuma ku bi mafi kyawun abinda aka saukar zuwa gareku daga Ubangijinku tun gabanin azaba ta zo muku ba tare da kunyi aune ba, kuma baku sani ba"

Waɗannan ayoyi dai suna nuna mana lallai ne mu gaggauta tuba daga zunubanmu, mu gyara halayenmu, mu koma ga Mahaliccinmu, tun kafin wannan dama ta kuɓce mana (tun kafin lokacin karɓan tuba ya wuce).

Shi yasa ma Manzon Allah ﷺ yake cewa: "Lallai Allah ﷻ Yana shimfiɗa HannunSa da dare saboda Karɓar Tuban wanda yayi laifi da rana, Yana kuma Shimfiɗa HannunSa da rana saboda Karɓar Tuban wanda yay laifi da dare, har zuwa sa'anda rana za ta fito ta mafaɗarta[108]"

Ya kai/ke mai karatu mai daraja! Inai mana wasiyyah da tsare dokokin Allah ﷻ da kuma jin tsoronsa.
Wannan it ace wasiyyar Allah ﷻ zuwa ga baki ɗaya bayinSa (tun daga kan mutanen farko har zuwa kanmu, ha ma zuwa na ƙarshen zuwa duniya) kamar yadda Yake cewa (cikin Suratun-Nisa'i daga ayah ta **131** zuwa ta **134**):

﴿ وَلِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلْأَرْضِ ۗ وَلَقَدْ وَصَّيْنَا ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْكِتَٰبَ مِن قَبْلِكُمْ وَإِيَّاكُمْ أَنِ ٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ ۚ وَإِن تَكْفُرُوا۟ فَإِنَّ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلْأَرْضِ ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ غَنِيًّا حَمِيدًا ﴿١٣١﴾ ﴾

"Kuma Allah ﷻ Shi Yake da Mulkin (baki ɗaya) abinda ke cikin sammai da (baki ɗaya) abinda yake cikin ƙassai. Kuma lallai haƙiƙa Munyi wasici ga waɗanda aka baiwa littafi gabaninku (har ma) da ku (kanku) akan cewa (dole) ku tsare dokokin Allah (ku ji tsoronSa). Idan kuma kuka kafirce (kuka kangare kuka ƙi bin wannan umurni), toh fa (ku sani) duk abinda yake cikin sammai da ƙassai baki ɗaya

[108] Sahih Muslim (Hadithi na 2759) daga Sahabi Abu-Musa Al-Ash'ariy (رضي الله عنه)

na Allah ne. Saboda haka Allah Ya kasance Mawadaci kuma Godajje Abin godiya (yadda imaninku ya kasance ba zai ƙare Shi da komai ba, haka nan rashin imaninku ma ba zai rage Shi da komai ba).

Ya ƙara tabbatar da cikar MulkinSa da kuma cikakken ikonSa akan komai, da kuma cikar wadatarsa, da kuma buƙatuwar baki ɗaya halittu zuwa gareShi Shi kaɗai, inda Yake cewa (cikin ayah ta gaba):

﴿وَلِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلْأَرْضِ ۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ وَكِيلًا ﴿١٣٢﴾﴾

"Kuma lallai Allah ﷻ Shi Yake da Mulkin (baki ɗaya) abinda ke cikin sammai da (baki ɗaya) abinda yake cikin ƙassai. Saboda haka Allah ﷻ Ya isa Ya zamto abin dogaro (Shi kaɗai ne Abin nufi da buƙata ga baki ɗaya halittunsa, Jallah Buwayi Gagara misali).

Saboda haka duk abinda muka aikata, toh fa kanmu mukayi wa. Shi kam Allah cikakken Mawadaci ne. Idan ma Ya ga dama cikin ƙasa da ƙiftawar ido Zai kawar da mu baki ɗayanmu Ya kawo wasu.

Hakan kuma ba komai ba ne a wajenShi. Domin kuwa Shi Mai cikakken iko ne akan dukkan komai.

Shi ne a ayah ta gaba sai Allah ﷻ Ya ƙara da cewa:

﴿إِن يَشَأْ يُذْهِبْكُمْ أَيُّهَا ٱلنَّاسُ وَيَأْتِ بِـَٔاخَرِينَ ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلَىٰ ذَٰلِكَ قَدِيرًا ﴿١٣٣﴾﴾

"Idan Ya ga dama Yana iya tafiyar da ku (Ya kawar da ku) ku dai waɗannan mutane, sannan kuma Ya taho da wasu (mutanen) na daban (Ya maye gurbinku da su). Kuma Allah ﷻ Ya kasance Mai (cikakken) iko ne akan hakan" KasancewarSa Mai cikakken iko akan komai da komai, Shi kaɗai Yake da ikon baiwa duk wanda Ya ga dama cikin bayinSa abinda Yake nema na duniya da lahira.

Da ma daga cikin bayi akwai wasu Salihan bayi waɗanda lahira suke so, ko da kuwa sun samu wani abu a duniya, toh suna amfani da shi wajen neman lahira. Irin waɗannan su ne masu tsira..
Akwai kuma waɗanda duniya kaɗai suke so. Ba su da rabo a lahira, saboda basu yi imani ba.
Toh duk wanda ka nema dai, babu wanda zai baka sai Allah ﷻ. Domin kuwa naShi ne Shi kaɗai, Bai da abokin tarayya. Kuma Yana bayarwa ne ga wanda Ya ga dama cikin bayinSa.
Wannan yake ƙara tabbatar da taɓewar masu dogaro akan wanin Allah.
Allah Ta'ala Ya tabbatar mana cewa komai da komai naShi ne, kuma Shi Yake baiwa wanda Yaga dama cikin bayinSa. Sannan kuma Ya ƙara tabbatar mana lallai duk wanda yayi aiki don duniya kaɗai, toh fa bai da rabo a lahira. Zai iya baiwa wanda Ya ga dama wani abu na duniya ɗin.
Wanda kuma yake neman lahira, toh shi ma sakamakonsa na Hannun Shi. Shi yasa a ayah ta gaba sai Yace:

﴿ مَّن كَانَ يُرِيدُ ثَوَابَ ٱلدُّنْيَا فَعِندَ ٱللَّهِ ثَوَابُ ٱلدُّنْيَا وَٱلْأَخِرَةِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ سَمِيعَۢا بَصِيرًا ﴿١٣٤﴾ ﴾

"Duk wanda ya kasance yana nufin (samun) sakamakon duniya ne, toh fa a wurin Allah ﷻ (kaɗai) sakamakon duniya (har ma) da na lahira yake. Kuma Allah ﷻ Ya kasance Mai (cikakken) ji, kuma Mai (cikakken) gani (Yana jin duk abinda kuke faɗa, kuma Yana ganin duk abinda kuke aikatawa, Yana kuma sane da duk abinda kuke ƙudurcewa a zukatanku, saboda haka Zai saka muku da duk abinda kuka aikata)".

**Waɗannan ayoyi masu daraja suna ƙunshe da darusa masu yawa. Kaɗan daga cikinsu su ne kamar haka:**

Suna ƙara tabbatar mana lallai Allah ﷻ Ya halicce mu ne ba don komai ba sai don mu kaɗaita Shi da bauta. Wannan bauta kuma dole ne muyi ta Yadda Shi Ya tsara kuma Yayi umurni, ba yadda muka ga dama ba.
Suna ƙara tabbatar mana lallai Shi fa Allah ﷻ ba wai Yana buƙatan wani abu ba ne daga garemu. Imanin masu imani ba zai ƙare Shi da komai ba. Haka nan ma duk kafircin kafirai ba zai rage Shi da komai ba. Shi cikakken mawadaci ne, mu ne muke buƙatan komai daga gareShi.
Sannan duk kyakkyawan aikinda muka aikata, toh fa garemu amfanin zai dawo. Haka kuma duk mumunan aikin da muka aikata, to akanmu sakamakon zai dawo. Kenan duk abinda muka shuka a nan duniya, to fa shi za mu girba a lahira. Saboda haka idan bawa ya samu Alkhairi a can, toh ya gode wa Allah domin kuwa Shi Ya datar da shi. Idan kuma Yaje ya tarar da sharri, toh kar ya zargi kowa sai kansa (domin kuwa shi ne haƙiƙanin sakamakon abinda ya ɓata lokacinsa a duniya yana ta aikatawa).
Saboda haka lallai ne mu zama masu taka-tsan-tsan a kullum. Mu tsare dokokin Allah, mu dage wajen aikata ayuka nagari (tun daga farillai har zuwa nafilfilu), mu nisanci saɓa wa Allah ﷻ, mu gaggauta tuba mu koma gareShi, mu kuma yawaita Istighfari a kullum, saboda fatan samun Rahamar Allah ﷻ.
Da fatan Allah Yasa mu dace da aikata abinda Zai Yarda da mu, Ya ƙara tabbatar da mu akan Tafarki madaidaici har mutuwa, yasa mu cika da imani, Ya kuma sa Aljannah Firdausi ce makomar mu a gobe ƙiyamah.

Haƙiƙa mai babban rabo a wajen Allah ﷻ daga cikin mutane, shi ne wanda zai yi tanadin guzuri tun yana da sauran dama.
Shi ne wanda zai shirya wa lahira tun kafin mutuwa ta sauko masa. Yana amfani da damar da Allah ﷻ Ya bashi don ganin ya shuka wa kansa Alkhairi kafin ya bar duniya.
Mara rabo a wajen Allah shi ne wanda yake wasa da damar da Allah ya bashi, shi ne wanda yake shagaltuwa da wasu al'amura na duniya (ya ƙi tsayawa ya bautawa Allah har lokaci Ya ƙure masa). Sai ya ga azaba ido da ido sannan yace wai zai tuba, a lokacinda hakan ba zai amfane shi da komai ba.
Da ma kuma bahaushe yace ba a fafe gora ranar tafiya, kamar yadda kuma ba a kiwon kare ranar farauta.
Sanannen abu ne garemu lallai mafi Alkhairin guzuri shi ne Tsoron Allah ﷻ. Da Tsoron Allah ne kaɗai bawa zai samu tsira a ranar tashin ƙiyama, ranar da dukiya da 'ya'yan da mutum ya tara ba za su amfane shi da komai ba.
Saboda haka lallai ne muji Tsoron Allah matuƙar jin tsoronSa, mu tsare dokokinSa, mu ƙara ƙaimi wajen yawaita ayukan ɗa'a, mu nisanci saɓo. Muyi riƙo da karantarwar Manzon Allah ﷺ. Mu yawaita Istighfari, mu Tuba mu koma ga Alla ﷻ. Shi kuma Allah ﷻ Ya yi Alƙawarin Zai mana Rahama matuƙar munyi hakan. Shi kuma Allah ﷻ ba Ya saɓa Alƙawari.
Idan har mun yarda cewa Alƙawarin Allah ﷻ gaskiya ne, toh fa lallai ne mu nemi YardarSa ta hanyar bin UmurninSa da kuma nisantar abinda Ya hanemu. Wannan kuma shi zai tabbatar da lallai ashe muna kyautata wa Allah ﷻ zato.
Manzon Allah ﷺ yace: "Kada ɗayanku ya mutu fahce (ya

dage ya yaƙi shaiɗan har ya zamto) yana mai kyautata zato ga Allah ﷻ".

Ya faɗi wannan magana ana sauran kwana uku kacal ya bar duniya (kamar yadda Sahabi Jabir ɗan Abdullahi ya faɗa, Allah Ya ƙara Yarda da su baki ɗaya). Wannan magana tana daga cikin manyan wasiyoyinda dole ne muyi riƙo dasu sosai don mu samu tsira a duniya da lahira. Domin kuwa tana cikin maganganun Manzon Allah ﷺ na ƙarshe-ƙarshe.

Allah Yasa nu dace.

Dukkan Yabo da Godiya marasa misaltuwa sun tabbata ga Allah Maɗaukaki, wanda Ya nuna mana ƙarshen wannan ɗan littafi cikin ƙoshin lafiya kamar yadda Ya nuna mana farkonsa.

Muna roƙon Allah ﷻ cikin RahmarSa Ya sanya mu cikin bayin nan naShi masu gaskiya cikin imaninsu, masu kyautata niyyah cikin furucinsu da ayukansu, masu yawan godiya gareShi gameda ni'imominSa, masu haƙuri da dangana gameda duk jarrabawar da ta same su, masu Tuban gaske zuwa gareShi daga dukkan laifukansu, kuma masu neman GafararSa daga dukkan zunubai.

Da fatan Allah Mai Jinƙai Ya karɓi Tuban mu, Ya Gafarta mana, Ya yafe mana, Yayi mana Jinƙai, mu da iyayenmu da 'ya'yanmu da Malamanmu da sauran 'yan-uwanmu Musulmi baki ɗaya. Allah Ya Gafarta mana, domin kuwa Shi Mai yawan Gafara ne kuma Mai Jinƙai.

Ya Allah Ka sanya mu cikin yardaddun bayinKa masu kyautata Ibada. Ka ƙara tabbatar damu akan Tafarki

Madaidaici har muutuwa, Ka tsare mu daga fitintinu da kuma azabar ƙabari, Ka tsare mu daga azabar wuta, Ka sa Aljannah ce makomar mu a gobe ƙiyamah.

Ya Allah Kayi daɗin Tsira da Aminci ga wannan bawa naKa kuma ManzonKa Annabi Muhammadu ﷺ, shi da Iyalansa da dukkan Sahabbansa, da sauran duk waɗanda suka biyo bayansu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako. Ameeen.

وَالسَّلاَمُ عَلَيْكُمْ وَرَحْمَةُاللّٰهِ وَبَرَكَاتُهُ